الجزء ٢١ الحزب ٤١

۞ وَلَا تُجَٰدِلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُ إِلَّا
ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنۡهُمۡۖ وَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱلَّذِيٓ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَأُنزِلَ
إِلَيۡكُمۡ وَإِلَٰهُنَا وَإِلَٰهُكُمۡ وَٰحِدٞ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ
٤٦ وَكَذَٰلِكَ أَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَۚ فَٱلَّذِينَ ءَاتَيۡنَٰهُمُ
ٱلۡكِتَٰبَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۖ وَمِنۡ هَٰٓؤُلَآءِ مَن يُؤۡمِنُ بِهِۦۚ وَمَا
يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا ٱلۡكَٰفِرُونَ ٤٧ وَمَا كُنتَ تَتۡلُواْ مِن
قَبۡلِهِۦ مِن كِتَٰبٖ وَلَا تَخُطُّهُۥ بِيَمِينِكَۖ إِذٗا لَّٱرۡتَابَ
ٱلۡمُبۡطِلُونَ ٤٨ بَلۡ هُوَ ءَايَٰتُۢ بَيِّنَٰتٞ فِي صُدُورِ ٱلَّذِينَ
أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَۚ وَمَا يَجۡحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا ٱلظَّٰلِمُونَ ٤٩ وَقَالُواْ
لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَٰتٞ مِّن رَّبِّهِۦۖ قُلۡ إِنَّمَا ٱلۡأٓيَٰتُ عِندَ ٱللَّهِ
وَإِنَّمَآ أَنَا۠ نَذِيرٞ مُّبِينٌ ٥٠ أَوَلَمۡ يَكۡفِهِمۡ أَنَّآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ
ٱلۡكِتَٰبَ يُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَرَحۡمَةٗ وَذِكۡرَىٰ
لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٥١ قُلۡ كَفَىٰ بِٱللَّهِ بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡ
شَهِيدٗاۖ يَعۡلَمُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۗ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ
بِٱلۡبَٰطِلِ وَكَفَرُواْ بِٱللَّهِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٥٢



**(46) kada ku yi muhawara - Ya ku Muminai - kada ku yi husuma, da Yahudu da Nasara, sai da salo mafi kyau, shi ne: hanyar kira zuwa ga Allah, da yin wa'azi da bada gamsassun dalilai, sai dai waxanda su ka yi zalunci, da taurin kai, da bijirewa gaskiya bayan sun gane ta, kuma suka yi fito na fito da ku, to waxannan ku yaqe su har sai sun miqa wuya, ko su bada jizya cikin qasqanci. Kuma ku faxa wa Yahudu da Nasara cewa: "Mun yi imani da abin da aka saukar mana na Alqur'ani, da kuma abin da aka saukar muku na Attaura da Injila, kuma mu da ku, abin bautar mu guda xaya ne, bashi da abokin tarayya a allantakarsa, ko rainon bayinsa, kuma mu masu biyayyane, da rankwafawa a gare shi.**

**(47) Kamar yadda muka saukar da littafi ga waxanda suka gabace ka, haka kai ma muka saukar maka da Alqur'ani. To wasu cikin masu karanta Attaura- kamar Abdullah bin Salam- suna yin imani da Alqur'ani, domin bayanan da littafansu suka yi a kansa. Daga cikin mushrikai ma akwai waxanda suke yin Imani da Alqur'ani. Babu wanda zai kafirce wa ayoyinmu sai Kafirai masu qin gaskiya bayan ta bayyana a gare su.**

**(48) Ya kai wannan Manzo, baka kasance gabanin saukar da Alqur'ani kana karanta wani littafi ba, kuma baka kasance kana rubutu da hannunka ba, domin baka iya karatu da rubutu ba, da ka iya, to da jahilai sun yi shakku cikin ingancin Annabtarka, kuma da sun ce daga littafan da suka gabata kake kwafowa.**

**(49) Tabbas Alqur'anin da aka saukar maka, ayoyi ne bayyanannu a cikin qirazan Muminai, ma'abota ilimi. Babu wanda zai qaryata ayoyin mu sai waxanda suka zalunci kansu, da kafircewa, da kuma bautawa wanin sa.**

**(50) Mushrikai suka ce: "Me ya hana a saukar wa Muhammad ayoyi daga Ubangijinsa?. Kamar yadda aka saukar wa Annabawan da suka gabace shi?". Ka gaya musu – Ya kai wannan Manzo - cewa: "Ayoyi duk a hannun Allah suke, yana saukar da su duk lokacin da ya ga dama, ba ni da ikon saukar da su, ni kawai mai gargaxin ku ne dangane da uqubarsa".**

**(51) Shin bai ishi waxannan masu neman ayoyi ba cewa: Mu muka saukar maka -Ya kai wannan Manzo - da Alqur'ani ana karanta musu, haqiqa a cikin Alqur'anin da aka saukar musu akwai jin qai da wa'azi ga masu yin imani, su ne waxanda zasu amfana da abin da yake ciki. Abin da aka saukar musu yafi alheri daga abin da aka saukarwa Manzanni a da.**

**(52) Ka ce - Ya kai wannan Manzo -: "Allah mai tsarki ya isa ya zama shaida a kan gaskiyar abin da na zo da shi, da kuma yadda kuka qaryata ni. Domin ya san duk abin da yake cikin sammai da qassai, babu wani abin da yake vuya a gare shi. Duk waxanda suka yi imani da vatattun abubuwan vata, kuma suka kafircewa Allah wanda ya cancanta a bauta masa shi kaxai, waxannan su ne asararru don sun riqi kafirci, sun yi watsi da imani".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Jayayya da ma'abota littafi, tana kasancewa ta hanya mafi kyau.**

**2 - Ana Imani da gaba xayan Manzanni, da littattafai, ba tare da bambancewa ba, yin hakan sharaxi ne na ingancin imani.**

**3 - Alqur'ani mai girma aya ce babba madawwamiya da take tabbatar da gaskiyar Annabtar Annabi (S. A. W)**

وَيَسۡتَعۡجِلُونَكَ بِٱلۡعَذَابِ وَلَوۡلَآ أَجَلٞ مُّسَمّٗى لَّجَآءَهُمُ ٱلۡعَذَابُ
وَلَيَأۡتِيَنَّهُم بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٥٣ يَسۡتَعۡجِلُونَكَ بِٱلۡعَذَابِ
وَإِنَّ جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةُۢ بِٱلۡكَٰفِرِينَ ٥٤ يَوۡمَ يَغۡشَىٰهُمُ ٱلۡعَذَابُ
مِن فَوۡقِهِمۡ وَمِن تَحۡتِ أَرۡجُلِهِمۡ وَيَقُولُ ذُوقُواْ مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ
٥٥ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ أَرۡضِي وَٰسِعَةٞ فَإِيَّٰيَ فَٱعۡبُدُونِ
٥٦ كُلُّ نَفۡسٖ ذَآئِقَةُ ٱلۡمَوۡتِۖ ثُمَّ إِلَيۡنَا تُرۡجَعُونَ ٥٧ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُبَوِّئَنَّهُم مِّنَ ٱلۡجَنَّةِ غُرَفٗا تَجۡرِي
مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ نِعۡمَ أَجۡرُ ٱلۡعَٰمِلِينَ ٥٨ ٱلَّذِينَ
صَبَرُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٥٩ وَكَأَيِّن مِّن دَآبَّةٖ لَّا تَحۡمِلُ
رِزۡقَهَا ٱللَّهُ يَرۡزُقُهَا وَإِيَّاكُمۡۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦٠ وَلَئِن
سَأَلۡتَهُم مَّنۡ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَ
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۖ فَأَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٦١ ٱللَّهُ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن يَشَآءُ مِنۡ
عِبَادِهِۦ وَيَقۡدِرُ لَهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ٦٢ وَلَئِن سَأَلۡتَهُم
مَّن نَّزَّلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَحۡيَا بِهِ ٱلۡأَرۡضَ مِنۢ بَعۡدِ مَوۡتِهَا
لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُۚ قُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِۚ بَلۡ أَكۡثَرُهُمۡ لَا يَعۡقِلُونَ ٦٣



**(53) Mushirikai suna yi maka gaggawa ya kai wannan Annabi (S. A. W), suna cewa: "A sauko musu da azabar da kake tsoratar da su ita". To su sani ba don Allah ya qaddara lokacin da azabar zata same su ba, da abin da suke nema ya zo musu, amma tabbas zai zo musu yana mai shammatarsu.**

**(54) Suna roqon ka ka gaggauto musu da azabar da kake yi musu alqawarinta, kuma haqiqa wutar Jahannama da Allah ya tanadar wa kafirai zata mamayesu, ba zasu iya gujewa azabarta ba.**

**(55) Ranar da azaba zata lulluvesu ta samansu, kuma ta zamo musu tamkar shimfixa ta qasan su, sai a ce musu cikin wulaqantarwa: "Ku xanxani sakamakon abin da kuka kasance kuna aikatawa na shirka da savo".**

**(56) Ya ku bayina da kuka yi imani da ni, ku yi hijira daga qasar da ba zaku iya bauta min ba, domin qasata mai yalwa ce, don haka ku bauta mini ni kaxai, kada ku haxa ni da kowa a wurin bauta.**

**(57) Kada tsoron mutuwa ya hana ku yin hijira, kowace rai sai ta xanxani mutuwa, kuma gare mu mu kaxai, za'a dawo da ku, ranar alqiyamah don ai muku hisabi.**

**(58) Kuma waxanda suka yi imani, sannan kuma suka yi ayyuka nagari, waxanda zasu kusantar da su ga Allah, to, tabbas zamu saukesu a wasu gidaje a cikin Aljannah, wanda qoramu ke gudana ta qarqashinsu, zasu dawwama a cikinsu, har abada, mutuwa ba zata samesu ba. Madalla da sakayyar masu yi wa Allah xa'a.**

**(59) Madalla da sakayyar masu yi wa Allah xa'a, masu haquri wurin biyayya, da barin savo, masu dogaro ga Ubangijinsu -shi kaxai- a cikin dukkan al'amuransu.**

**(60) Dukkanin dabbobi, duk yawansu, baza su iya tattare arzikinsu ba, ko xaukarsa. Allah ne mai azurta su, da kuma ku. Don haka baku da wani uzuri wurin qin yin hijira, saboda gudun yunwa. Shi ne mai jin maganganun ku, masanin qudure-qudiren ku, da ayyukan ku, babu abin da yake kuvuce masa, kuma zai muku sakayya a kan hakan.**

**(61) Ya kai wannan Manzo, da a ce zaka tambayi waxannan mushirikai cewa: "Wane ne ya halicci sammai da qassai? Wane ne ya hore rana da wata, wannan na bin wannan? Tabbas zasu ce: "Allah ne". To, ta yaya ake kawar da hankulan su ga barin imani da shi, shi kaxai? Kuma suke bautawa wasu gumakan da basa amfanarwa ko cutarwa?".**

**(62) Shi ne yake yalwata arziki ga wanda ya ga dama cikin bayinsa, kuma ya kuntata arzikin wanda ya ga dama, domin wata hikima da shi kaxai ne ya santa. Haqiqa Allah masani ne ga komai, babu wani abu da yake vuya a gare shi.**

**(63) Ya kai wannan Manzo, da a ce zaka tambayi mushirikai: "Wane ne ya saukar da ruwan sama? ya fitar da tsirrai daga gare shi bayan ta bushe?" Tabbas da zasu ce "Allah ne". To ka ce - Ya kai wannan Manzo -: "Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya bayyana hujja a kanku, sai dai da yawan su ba sa hankalta, domin da a ce suna hankalta, ai da basu haxa gumakan da basa cutarwa ko amfanarwa a wurin bauta ba".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Gaggawar da kafiri yake yi don a sauko masa da azaba, yana tabbatar da wautarsa.**
**2 - Qofar yin hijira domin kuvuta da addini a buxe take.**
**3 - Falalar haquri, da dogaro ga Allah.**
**4 - Tabbatar da ayyukan Allah tare da watsi da bauta masa, baya jawo wa ma'abocin sa tsira, ko zama mai imani.**

وَمَا هَٰذِهِ الْحَيَوٰةُ الدُّنْيَا إِلَّا لَهْوٌ وَلَعِبٌ ۚ وَإِنَّ الدَّارَ الْآخِرَةَ لَهِيَ
الْحَيَوَانُ ۚ لَوْ كَانُوا يَعْلَمُونَ ٦٤ فَإِذَا رَكِبُوا فِي الْفُلْكِ دَعَوُا اللَّهَ
مُخْلِصِينَ لَهُ الدِّينَ فَلَمَّا نَجَّاهُمْ إِلَى الْبَرِّ إِذَا هُمْ يُشْرِكُونَ ٦٥
لِيَكْفُرُوا بِمَا آتَيْنَاهُمْ وَلِيَتَمَتَّعُوا ۖ فَسَوْفَ يَعْلَمُونَ ٦٦
أَوَلَمْ يَرَوْا أَنَّا جَعَلْنَا حَرَمًا آمِنًا وَيُتَخَطَّفُ النَّاسُ مِنْ
حَوْلِهِمْ ۚ أَفَبِالْبَاطِلِ يُؤْمِنُونَ وَبِنِعْمَةِ اللَّهِ يَكْفُرُونَ ٦٧
وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ افْتَرَىٰ عَلَى اللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِالْحَقِّ لَمَّا جَاءَهُ ۚ
أَلَيْسَ فِي جَهَنَّمَ مَثْوًى لِلْكَافِرِينَ ٦٨ وَالَّذِينَ جَاهَدُوا
فِينَا لَنَهْدِيَنَّهُمْ سُبُلَنَا ۚ وَإِنَّ اللَّهَ لَمَعَ الْمُحْسِنِينَ ٦٩

آياتها ٦٠ — سُورَةُ الرُّومِ — ترتيبها ٣٠

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

ربع الحزب ٤١ الم ١ غُلِبَتِ الرُّومُ ٢ فِي أَدْنَى الْأَرْضِ وَهُمْ مِنْ
بَعْدِ غَلَبِهِمْ سَيَغْلِبُونَ ٣ فِي بِضْعِ سِنِينَ ۗ لِلَّهِ الْأَمْرُ
مِنْ قَبْلُ وَمِنْ بَعْدُ ۚ وَيَوْمَئِذٍ يَفْرَحُ الْمُؤْمِنُونَ ٤
بِنَصْرِ اللَّهِ ۚ يَنْصُرُ مَنْ يَشَاءُ ۖ وَهُوَ الْعَزِيزُ الرَّحِيمُ ٥



**(64) Wannan rayuwar ta duniya da abubuwan da ta qunsa na kayan sha'awa, ba komai ba ne face ruxi ga zukatan da suka rataya da su, ba wani lokaci mai tsawo zasu xauka zasu qare ba, amma rayuwar lahira ita ce madawwamiya, kuma da a ce sun san hakan da basu fifita abu mai qarewa ba a kan madawwami. Yayin da Allah ya yi bayanin tufka da warwarar mushirikai, yayin da suka yi imani da ayyukan Allah, idan an tambaye su waye ya halicci sammai da qassai, suka kuma kafircewa bauta wa Allah shi kaxai, suke bautawa waninsa, sai Allah ya sake bayanin wata tufka da warwarar ta su, yayin da suke tsarkake Allah shi kaxai, idan suna jin tsoron nutsewa, da kuma yadda suke komawar cikin shirka, suna bautawa wasu allolin tare da shi, yayin da ya tseratar daga nutsewa. Ya ce: (65) Idan mushirikai suka hau jiragen ruwa a cikin teku, sai su kira Allah kaxai, suna masu tsarkake addu'a a gare shi, a kan ya tseratar da su daga nutsewa, yayin da ya tseratar da su sai su qara dawowa mushirikai, suna kiran allolinsu tare da shi. (66) Sun koma yin shirka don butulci ga abin da muka basu na ni'ima, kuma don su ji daxi da abin da aka ba su na qawar duniya, to, da sannu zasu san mummunan qarshensu, yayin da zasu mutu. (67) Shin waxannan masu kangarewa da butulcewa ni'imomin Allah a yayin da ya kuvutar da su daga nutsewa a teku, basu ga wata ni'imar da ya daxa musu ba, ita ce: Mun sanya musu garin makkah cikin aminci game da jininsu,da dukiyoyinsu,alhalin ga wasun su ana kai musu hari, a kashe su,a kame su, a bautar da matansu, a kwashe dukiyoyinsu, yanzu da allolinsu na qarya za su yi imani? Kuma da ni'imomin za su kafirce, baza su gode wa Allah ba?. (68) Babu wanda ya kai zaluncin mutumin da ya qirqiri qarya ga Allah ta hanyar jingina masa abokin tarayya, ko qaryata gaskiyar da Annabinsa (S. A. W) ya zo da ita. Babu kokwanto cewa a cikin wutar Jahannama akwai masauki ga kafirai da makamantan su.**
**(69) Duk waxanda suka jajirce da kawunansu wurin neman yardar mu, lallai zamu datar dasu ga tafarki madaidaici. Haqiqa Allah yana tare da masu kyautatawa, da taimakon sa, da kuma shiriyar sa.**

# Suratur Rum

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar: Bayanin yadda haqiqanin lamarin halitta yake, ta yadda Jujjuya al'amura da abubuwa da dukkan komai yake hannun Allah, kamar yadda Allah Maxaukakin Sarki ya ce, "Lamarin gaba xaya na Allah tun farko da kuma qarshe".**

**Tafsir: (1) (Alif, Laam, Meem). Bayani ya gabata a kan ire-iren waxannan haruffa farkon Suratul Baqara.**
**(2) Farisawa sun samu galaba a kan Rumawa. (3) A wani wuri da yake kusa da garin Sham fiye da garin Farisa, kuma Rumawa za su ci galaba a kan Farisawa, bayan galabar da Farisawa suka ci a kansu**
**(4) Duk a lokacin da bai gaza shekara uku ba, kuma ba zai wuce shekara goma ba, lamari duka a hannun Allah yake gabanin samun galabar Rumawa da bayanta, kuma a ranar da Rumawa zasu yi galaba a kan Farisawa, Muminai za su yi farin ciki. (5) Zasu yi farin ciki da taimakon Allah ga Rumawa, don su ma'abota littafi ne. Allah yana bada nasara ga wanda ya ga dama, a kan wanda ya ga dama. Shi ne mabuwayin da ba a rinjayarsa, kuma shi mai jinqai ne ga bayin sa Muminai.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Komawar mushrikai ga Allah a lokacin tsanani, suna masu mancewa da gumakan su, kuma yadda suke yin shirka da shi a lokacin yalwa, wannan dalili ne a kan hauragiyar su. 2 - Jihadi domin xaukaka kalmar Allah sababi ne na samun dacewa ga gaskiya. 3 - Labaran da Alqur'ani yake bayarwa na gaibu dalili ne a kan cewa, shi wannan Alqur'ani daga wajen Allah yake.**

وَعۡدَ ٱللَّهِۖ لَا يُخۡلِفُ ٱللَّهُ وَعۡدَهُۥ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ
٦ يَعۡلَمُونَ ظَٰهِرٗا مِّنَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُمۡ عَنِ ٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ
غَٰفِلُونَ ٧ أَوَلَمۡ يَتَفَكَّرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۗ مَّا خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَآ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَأَجَلٖ مُّسَمّٗىۗ وَإِنَّ كَثِيرٗا
مِّنَ ٱلنَّاسِ بِلِقَآيِٕ رَبِّهِمۡ لَكَٰفِرُونَ ٨ أَوَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي
ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُوٓاْ
أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَأَثَارُواْ ٱلۡأَرۡضَ وَعَمَرُوهَآ أَكۡثَرَ مِمَّا
عَمَرُوهَا وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ
لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٩ ثُمَّ كَانَ
عَٰقِبَةَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ ٱلسُّوٓأَىٰٓ أَن كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَكَانُواْ
بِهَا يَسۡتَهۡزِءُونَ ١٠ ٱللَّهُ يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ ثُمَّ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ
١١ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُبۡلِسُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ١٢ وَلَمۡ يَكُن لَّهُم مِّن
شُرَكَآئِهِمۡ شُفَعَٰٓؤُاْ وَكَانُواْ بِشُرَكَآئِهِمۡ كَٰفِرِينَ
١٣ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يَوۡمَئِذٖ يَتَفَرَّقُونَ ١٤ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَهُمۡ فِي رَوۡضَةٖ يُحۡبَرُونَ ١٥



**(6) Wannan cin nasarar alqawari ne daga Allah, kuma da tabbatuwar sa ne Muminai zasu qara samun sakankancewa da Allah, a kan alqawarin da yake yi na taimako. Amma mafi yawan mutane baza su fahimci haka ba saboda kafircinsu.**

**(7) Basu san meye imani, ko hukunce-hukuncen shari'ah ba, kawai dai sun san zahiri daga rayuwar duniya ne, ta fuskar neman abinci, da gina rayuwar duniya, amma su game da lahira, wadda ita ce gida na haqiqa, masu bijirewa ne, basa kallonta kwata-kwata.**

**(8) Waxannan mushirikai, masu qaryatawa ba zasu yi tunani a kan kansu, ta yaya Allah ya halicce su, ta yaya halicci sauran abubuwa. Allah bai halicci Sammai da qassai ba sai da gaskiya, bai haliccesu don wasa ba, kuma ya sanya musu wani lokaci qayyadajje na zaman su a duniya, sai dai da yawa daga cikin mutane masu kafircewa haxuwa da Ubangijin su ne ranar alqiyama, don haka basa yin wani shiri da aiki nagari,wanda zasu samu yarda a wurin Ubangijinsu.**

**(9) Yanzu waxannan ba zasu yi tafiya a bayan qasa ba, don su lura cewa: yaya qarshen masu qaryatawa gabanin su ya kasance, haqiqa waxannan al'ummatai sun fi su karfi, kuma sun jujjuya qasa don yin noma, da raya ta, sama da yadda al'ummarka suke raya ta, kuma Manzannin su sun zo musu da hujjoji bayyanannu, a kan kaxaita Allah, amma sai suka qaryata su, Allah bai zaluncesu ba yayin da ya halakar da su, sai dai kawunansu suka kasance suna zalunta, saboda jefa su cikin halaka a dalilin kafircinsu.**

**(10) Sai qarshen waxanda ayyukansu suka munana, saboda shirka da Allah da munanan ayyuka ya zama mummunan qarshe, saboda sun qaryata ayoyin Allah, kuma suna izgili da su, kuma suna musu izgili.**

**(11) Allah shi ne ya fari halitta ba tare da ya ga samfuri a wurin wani ba, sannan shi ne yake rasar da ita, sannan ya dawo da ita, sannan gare shi, shi kaxai zaku koma, don ya yi muku hisabi da sakamako ranar alqiyama.**

**(12) Ranar da alqiyama zata tsaya, masu laifi zasu yanke qauna daga rahamar Allah, kuma abin da suke buri ya yanke, saboda da yankewar hujjarsu a kan kafircewarsu da Allah.**

**(13) Basu da wasu masu ceto daga a cikin abokan tarayyarsu, waxanda suke bautawa a duniyu, waxanda zasu cece su don fitar da su daga azaba, kuma sun kasance masu kafircewa abokan tarayyarsu, sun tavar da su a yayin da suka fi buqatarsu, saboda sun kasance daidai da juna cikin halaka.**

**(14) A ranar da alqiyama zata tsaya, mutane zasu rarraba a wajen sakamako, gwargwadon ayyukansu a duniya, wasu a xaukaka su zuwa "illiyyuna", wasu kuma a qasqantar da su zuwa "Asfalas Safilin".**

**(15) Amma waxanda suka yi imani, kuma suka yi aiki nagari, waxanda Allah ya yarda da su, to waxannan zasu kasance a gidan Aljanna, ana faranta musu rai, da abin da yake samunsu a cikinta na ni'ima dauwamammiya, wadda bata yankewa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sanin abin da zai gyara duniya kaxai, tare da gafala daga abin da zai gyara lahira ba, ba shi da amfani.**
**2 - Ayoyin Allah da suke cikin rayukan bayin da ya halitta, da kuma sasannin duniya sun isa su zama dalilai gamsassu a kan kaxaitakarsa.**
**3 - Zalunci shi ne sababin da ya sa aka halakar da mutanen da suka gabata.**
**4 - Ranar alqiyama Allah zai xaukaka Muminai, ya qasqantar da kafirai.**

وَأَمَّا ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا وَلِقَآيِٕ ٱلۡأٓخِرَةِ
فَأُوْلَٰٓئِكَ فِي ٱلۡعَذَابِ مُحۡضَرُونَ ١٦ فَسُبۡحَٰنَ ٱللَّهِ حِينَ تُمۡسُونَ
وَحِينَ تُصۡبِحُونَ ١٧ وَلَهُ ٱلۡحَمۡدُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ
وَعَشِيّٗا وَحِينَ تُظۡهِرُونَ ١٨ يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ
ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَيُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۚ وَكَذَٰلِكَ تُخۡرَجُونَ
١٩ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنۡ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ إِذَآ أَنتُم بَشَرٞ
تَنتَشِرُونَ ٢٠ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنۡ خَلَقَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ
أَزۡوَٰجٗا لِّتَسۡكُنُوٓاْ إِلَيۡهَا وَجَعَلَ بَيۡنَكُم مَّوَدَّةٗ وَرَحۡمَةًۚ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٢١ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ
خَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱخۡتِلَٰفُ أَلۡسِنَتِكُمۡ وَأَلۡوَٰنِكُمۡۚ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّلۡعَٰلِمِينَ ٢٢ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ مَنَامُكُم
بِٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ وَٱبۡتِغَآؤُكُم مِّن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ٢٣ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ يُرِيكُمُ ٱلۡبَرۡقَ
خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَيُنَزِّلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَيُحۡيِۦ بِهِ ٱلۡأَرۡضَ
بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٢٤



**(16) Kuma waxanda suka kafirce wa Allah, suka qaryata ayoyinmu, waxanda muka saukar wa Manzanmu, suka qaryata tashi bayan mutuwa, da kuma sakamako, to waxannan za a zo da su don a azabtar da su, azabar da zata lazimce su.**

**(17) Ku tsarkake Allah yayin da kuke shiga yammaci, shi ne lokacin sallar magriba da isha'i. kuma ku tsarkake shi lokacin da kuke shiga safiya, shi ne lokaci sallar asuba.**

**(18) Shi kaxai ya cancanta a yi wa yabo da kirari. Mala'iku a cikin sammai suna gode masa, halittunsa a cikin qassai suna gode masa, don haka ku tsarkake shi yayin da kuka kai lokacin la'asar, hakanan ku tsarkake a lokacin da kuke shiga lokacin azahar.**

**(19) Shi ne yake fitar da rayayye daga matacce, kamar fitar da mutum da digon maniyyi, ko dan tsako daga qwai, haka nan shi yake fitar da matacce daga rayayye, kamar fitar da digon maniyyi daga mutum, ko kuma qwai daga kaza, kuma shi ne yake raya qasa bayan ta mutu, ta hanyar sauko da ruwan sama, da fito da tsirrai, to kamar haka kuma zaku fito daga qaburburan ku, domin a yi muku hisabi.**

**(20) Daga cikin ayoyin Allah masu girma, da suke tabbatar da ikonsa, da kaxaitakar sa: shi ne ya halicce ku ya ku mutane daga turvaya, a yayin da halicci babanku daga tavo, sai ga shi kuma kun zama mutane qaruwa ta hanyar haihuwa, kuna watsuwa a mahudar rana da kuma mafaxarta.**

**(21) Yana daga cikin ayoyinsa masu girma, da suke tabbatar da ikonsa, da kaxaitakar sa: shi ne ya halitta muku – mazaje- daga jinsin ku matayen aure, domin rayukan ku su samu nutsuwa da su, domin zama tare da su, kuma ya sanya qauna, da tausayi a tsakanin ku da su. Tabbas cikin abin da aka faxa, akwai dalilai mabayyana ga mutanen da suke da hankali. Domin su ne suke iya cin gajiyar hankulan su.**

**(22) Yana daga cikin ayoyin sa masu girma, da suke tabbatar da ikon sa, da kaxaitakar sa halittar sammai da qassai, da kuma bambanci harshenku, da bambancin launinku.Tabbas cikin abin da aka faxa, akwai dalilai da hujjoji bayyanannu ga masu ilimi da basira.**

**(23) Yana daga cikin ayoyin sa masu girma, da suke tabbatar da ikon sa, da kaxaitakar sa barcin da kuke yi cikin dare, da kuma wanda ku keyi da rana, domin ku samu hutu daga wahalhalun da kuka yi wurin aiki. Kuma ya sanya muku yini domin ku fita neman arziki daga Ubangijin ku. Tabbas cikin abin da aka faxa, akwai dalilai bayyanannu ga mutanen da suke ji, ji irin na lura, da karvar abin da aka ji.**

**(24) Yana daga cikin ayoyin sa masu girma, da suke tabbatar da ikonsa, da kaxaitakar sa yana nuna muku walqiya a sama, ya haxa tsoron tsawar da kwaxayin saukar ruwa a cikinta, sai ya saukar muku da ruwan sama, ya raya qasa bayan ta bushe, ta hanyar fitar da tsirrai daga cikinta. Tabbas a cikin abin da aka fada, akwai dalilai bayyanannu ga mutanen da suke hankalta, domin da wannan ne zasu kafa hujja a kan yiwuwar tashin alqiyama bayan mutuwa, domin yin hisabi, da kuma sakamako.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Bawa ya raya lokutan sa da yin sallah, da tasbihi, alama ce da take nuna kyakkyawan qarshe.**

**2 - Kafa hujja a kan yiwuwar tashin alqiyama ta fuskar yadda rayuwa take sabunta, kuma take canjawa, ta yadda yake halittar rayayye daga matacce, da kuma matacce daga rayayye.**

**3 - Ayoyin Allah a cikin halittar sa, da kuma duniya ba kowa yake amfanuwa da su ba, sai wanda ya yi amfani da hanyoyin fahimtar sa, na fili da na voye, waxanda Allah ya yi masa ni'ima da su.**

وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن تَقُومَ ٱلسَّمَآءُ وَٱلۡأَرۡضُ بِأَمۡرِهِۦۚ ثُمَّ إِذَا دَعَاكُمۡ
دَعۡوَةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ إِذَآ أَنتُمۡ تَخۡرُجُونَ ٢٥ وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۖ كُلّٞ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ٢٦ وَهُوَ ٱلَّذِي يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ
يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهۡوَنُ عَلَيۡهِۚ وَلَهُ ٱلۡمَثَلُ ٱلۡأَعۡلَىٰ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢٧ ضَرَبَ لَكُم مَّثَلٗا
مِّنۡ أَنفُسِكُمۡۖ هَل لَّكُم مِّن مَّا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُم مِّن
شُرَكَآءَ فِي مَا رَزَقۡنَٰكُمۡ فَأَنتُمۡ فِيهِ سَوَآءٞ تَخَافُونَهُمۡ
كَخِيفَتِكُمۡ أَنفُسَكُمۡۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ
يَعۡقِلُونَ ٢٨ بَلِ ٱتَّبَعَ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَهۡوَآءَهُم بِغَيۡرِ عِلۡمٖۖ
فَمَن يَهۡدِي مَنۡ أَضَلَّ ٱللَّهُۖ وَمَا لَهُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٢٩ فَأَقِمۡ
وَجۡهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفٗاۚ فِطۡرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيۡهَاۚ
لَا تَبۡدِيلَ لِخَلۡقِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ
نصف الحزب ٤١ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٣٠ ۞ مُنِيبِينَ إِلَيۡهِ وَٱتَّقُوهُ وَأَقِيمُواْ
ٱلصَّلَوٰةَ وَلَا تَكُونُواْ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٣١ مِنَ ٱلَّذِينَ فَرَّقُواْ
دِينَهُمۡ وَكَانُواْ شِيَعٗاۖ كُلُّ حِزۡبِۢ بِمَا لَدَيۡهِمۡ فَرِحُونَ ٣٢



**(25) Yana daga cikin ayoyin Allah masu girma, da suke tabbatar da ikonsa, da kaxaitakar sa, tsayawar sama, ba tare da ta faxo ba, da kuma tsayawar qasa, ba tare da ta rushe ba, duk wannan da umarnin Ubangiji ne. sannan kuma idan Allah mai tsarki ya kirawo ku daga bayan qasa, ta hanyar yin busa a qaho, sai ka ga kuna fitowa daga qaburburanku domin yi muku hisabi, da kuma sakamako.**

**(26) Duk abin da yake cikin sammai da qassai mallakin Allah ne, kuma halittarsa ne, kuma shi ya qaddare shi, kuma gare shi suke yin biyayya, kuma suke miqa lamarinsu.**

**(27) Allah mai tsarki shi ne wanda ya fari halitta, ba tare da ya ga samfur a wurin wani ba, kuma shi ne zai dawo da halittar bayan ta qare, kuma dawo da halittar ya fi masa sauqi a kan samar da ita a farko, duk guda biyun masu sauqi ne a wurinsa, domin idan yana son wani abu ya kasance cewa yake yi: "kasance" sai ya kasance. Kuma duk wata siffa ta girma da kamala, ta qololuwa, gare shi ta tabbata. Shi ne mabuwayin da ba a rinjayar sa, mai hikima cikin halittarsa da gudanarwarsa.**

**(28) Ya ku mushirikai, Allah ya buga muku misali daga kawunanku, shin a bayin ku, da abubuwan da kuka mallaka, akwai wani da ya yi tarayya da ku a cikin dukiyoin ku? Shin kuna jin tsoron su raba dukiyoyin ku, tare da ku? Kamar yadda sashenku suke tsoron abokan hulxarsu kada su raba dukiyar su daidai da daidai? Tabbas ba zaku yarda da haka ba. To Allah ya fi ku cancanta da hakan a cikin mulkinsa. Kuma ta hanyar buga waxannan misalai ne muke bayyan hujjoji mabambanta ga mutanen da suke hankalta, domin su ne suke amfanuwa da haka.**

**(29) Takaitawa cikin hujjoji ba shi ne sababin halakar su ba, kuma ba rashin yin bayani ba ne, kawai son zuciya ne, da makuniyar biyayya ga iyaye da kakanni. Waye zai datar da wanda Allah ya vatar da shi ga barin shiriya? Babu wanda ya isa. Kuma babu wanda zai kare su daga azabar Allah.**

**(30) Ya kai wannan Manzo ka fuskanci addinin da aka fuskantar da kai gare shi, da kai da waxanda suke tare da kai., kuna masu kaucewa dukkanin wasu addinai. Addinin musulunci shi ne addinin da Allah ya halicci mutane a kansa, babu canjawa ga halittar Allah. Wannan shi ne addini miqaqqe, amma da yawa daga cikin mutane basu san haka ba.**

**(31) Ku koma gare shi maxaukakin sarki, kuna masu tuba daga zunubanku. Ku ji tsoronsa ta hanyar aikata umarninsa, da kuma nisantar haninsa, ku cika sallah bisa sifa mafi kamala, kada ku kasance cikin mushirikai, su ne waxanda suke warware asalin yadda aka halicce su da yin shirka da Allah a cikin bautarsu.**

**(32) Kada ku kasance cikin mushirikai, waxanda suka canza addininsu, suka yi imani da sashensa, suka kuma bijirewa sashe, suka zama qungiya qungiya, kowace qungiya cikinsu mai farin ciki ce da abin da take kai na vata, tana ganin ita kaxai ce kawai a kan daidai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sunkuyawar dukkanin halittu ga Allah, ko dai bisa zavi, ko kuma ta dole.**
**2 - Kafa hujja da halittar farko a kan tashi bayan mutuwa, hujja ce bayyananniya.**
**3 - Biyewa son zuciya yana vatarwa, kuma yana sanya xagawa.**
**4 - Addinin musulunci, addini ne da ya dace da lafiyayyen hankali**

وَإِذَا مَسَّ ٱلنَّاسَ ضُرٌّ دَعَوْا۟ رَبَّهُم مُّنِيبِينَ إِلَيْهِ ثُمَّ إِذَآ أَذَاقَهُم
مِّنْهُ رَحْمَةً إِذَا فَرِيقٌ مِّنْهُم بِرَبِّهِمْ يُشْرِكُونَ ٣٣ لِيَكْفُرُوا۟ بِمَآ
ءَاتَيْنَٰهُمْ ۚ فَتَمَتَّعُوا۟ فَسَوْفَ تَعْلَمُونَ ٣٤ أَمْ أَنزَلْنَا عَلَيْهِمْ
سُلْطَٰنًا فَهُوَ يَتَكَلَّمُ بِمَا كَانُوا۟ بِهِۦ يُشْرِكُونَ ٣٥ وَإِذَآ أَذَقْنَا
ٱلنَّاسَ رَحْمَةً فَرِحُوا۟ بِهَا ۖ وَإِن تُصِبْهُمْ سَيِّئَةٌۢ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ
إِذَا هُمْ يَقْنَطُونَ ٣٦ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَبْسُطُ ٱلرِّزْقَ لِمَن يَشَآءُ
وَيَقْدِرُ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ ٣٧ فَـَٔاتِ ذَا ٱلْقُرْبَىٰ
حَقَّهُۥ وَٱلْمِسْكِينَ وَٱبْنَ ٱلسَّبِيلِ ۚ ذَٰلِكَ خَيْرٌ لِّلَّذِينَ يُرِيدُونَ
وَجْهَ ٱللَّهِ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ٣٨ وَمَآ ءَاتَيْتُم مِّن رِّبًا
لِّيَرْبُوَا۟ فِىٓ أَمْوَٰلِ ٱلنَّاسِ فَلَا يَرْبُوا۟ عِندَ ٱللَّهِ ۖ وَمَآ ءَاتَيْتُم مِّن
زَكَوٰةٍ تُرِيدُونَ وَجْهَ ٱللَّهِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُضْعِفُونَ ٣٩
ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ ثُمَّ رَزَقَكُمْ ثُمَّ يُمِيتُكُمْ ثُمَّ يُحْيِيكُمْ ۖ هَلْ مِن
شُرَكَآئِكُم مَّن يَفْعَلُ مِن ذَٰلِكُم مِّن شَىْءٍ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ
عَمَّا يُشْرِكُونَ ٤٠ ظَهَرَ ٱلْفَسَادُ فِى ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ بِمَا كَسَبَتْ
أَيْدِى ٱلنَّاسِ لِيُذِيقَهُم بَعْضَ ٱلَّذِى عَمِلُوا۟ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ٤١



**33 Idan wani tsanani na rashi lafiya, ko talauci, ko fari, ya smu mushirikai, sai su kira Ubangijinsu mai tsarki shi kaxai, suna masu komawa zuwa gare shi da qanqan da kai, domin ya yaye musu cutar da ta same su. Amma idan ya yaye musu, ya jiqansu, sai ka ga wata jama'a daga cikinsu sun koma yin shirkarsu, suna masu kiran wanin Allah a wurin addu'ar su.**

**34 Idan suka kafircewa ni'imar Allah, wadda daga cikinta akwai ni'imar yaye musu cuta, suka ci gaba da jin daxi da abin da yake gabansu a wannan rayuwa, to da sannu zasu gani ranar alqiyama cewa lallai sun kasance cikin vata mabayyani.**

**35 Me ya sa suka yi shirka da Allah alhali babu su da wata hujja? Kuma bamu saukar musu da wata hujja a wani littafi da zasu kafa hujja da shi a kan shirkar su ba, kuma babu wani littafi tare da su da yake magana a kan shirkarsu ba, ya tabbatar da ingancin abin da suke kai na kafirci.**

**36 Idan muka xanxanawa mutane wata ni'ima, daga cikin ni'imomin mu, kamar lafiya, da wadata, sai su yi fariya da ita, suna masu yin girman kai, amma idan abu maras daxi ne ya same su, kamar rashin lafiya, talauci saboda abin da hannanyen su suka jawo musu na savon Allah, sai ka ga suna yanke qauna daga rahamar Allah, suna xebe qauna daga gushewar abin da yake munana musu.**

**37 Shin basu ga yadda Allah yake yalwata arziki ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa ba, don jarrabawa ga bawan, shin zai gode, ko zai yi butulci? kuma ya quntata arziki ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, don jarrabawa a gare shi, ya ga shin zai yi haquri, ko kuwa zai yi fushi?. Tabbas cikin yalwata arziki ga wasu, da kuma quntata shi ga wasu, akwai dalilai ga Muminai a kan tausayin Allah da jinqansa.**

**38 Ya kai musulmi, ka ba makusancinka abin da ya cancance shi na alheri da zumunci, kuma ka ba mabuqaci abin da zai biya buqatarsa da shi, ka ba wa baqo, wanda guzurinsa ya yanke, wannan bayarwar ga waxannan vangarori, ita ta fi alheri, ga waxanda suke neman yardar Allah, waxanda suke gabatar da wannan taimako da haqqoqi, su ne waxanda zasu rabauta da samun abin da suke so na Aljanna, da kuvuta daga abin da su ke tsoro na azaba.**

**39 Duk abin da kuka bawa wani daga cikin mutane na dukiya, don ya dawo muku da abin da kuka ba shi da qari, to ladan ba zai daxu ba a wurin Allah. Amma duk abin da kuka bayar na dukiya ga wanda zai kawar da wata buqata tasa, kuna neman lada a wurin Allah, ba kwa neman wani matsayi ko lada a wurin mutane ba, to lallai waxannan su ne waxanda ake ninka musu lada a wurin Allah.**

**40 Allah ne kaxai ya kaxaita da halittar ku, da azurta ku, da kashe ku, da raya ku bayan mutuwa. To shin a cikin gumakanku waxanda kuke bauta musu akwai wanda zai iya yin wani abu daga cikin wannan? Allah ya tsarkaka, kuma ya girmama, daga abin da mushirikai suke faxa da qudurcewa game da shi.**

**41 Varna ta bayyana a kan tudu, da cikin ruwa, a cikin rayuwar mutane ta hanyar tawayar rayuwar, da cikin kawunansu ta hanyar rashin lafiya, da annoba, saboda abubuwan da suke aikatawa na savo, wannan ya bayyana don Allah ya xanxana musu wani vangare na sakamakon munanan ayyukansu, da fatan ko zasu dawo gare shi su tuba.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yin fariya yayin ni'ima, da kuma xebe qauna daga rahama yayin azaba, siffofi ne guda biyu na kafirai. 2 - Ba wa ma'abota haqqi haqqinsu yana janyo rabauta. 3 - Shafe albarka riba, da ninka ladan ciyarwa saboda Allah. 4 - Tasirin zunubai wurin yaxuwar annoba, da lalacewar yanayi.**

قُلْ سِيرُوا۟ فِى ٱلْأَرْضِ فَٱنظُرُوا۟ كَيْفَ كَانَ عَـٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلُ ۚ
كَانَ أَكْثَرُهُم مُّشْرِكِينَ ﴿٤٢﴾ فَأَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ ٱلْقَيِّمِ مِن
قَبْلِ أَن يَأْتِىَ يَوْمٌ لَّا مَرَدَّ لَهُۥ مِنَ ٱللَّهِ ۖ يَوْمَئِذٍ يَصَّدَّعُونَ ﴿٤٣﴾ مَن
كَفَرَ فَعَلَيْهِ كُفْرُهُۥ ۖ وَمَنْ عَمِلَ صَـٰلِحًا فَلِأَنفُسِهِمْ يَمْهَدُونَ ﴿٤٤﴾
لِيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّـٰلِحَـٰتِ مِن فَضْلِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ
ٱلْكَـٰفِرِينَ ﴿٤٥﴾ وَمِنْ ءَايَـٰتِهِۦٓ أَن يُرْسِلَ ٱلرِّيَاحَ مُبَشِّرَٰتٍ وَلِيُذِيقَكُم
مِّن رَّحْمَتِهِۦ وَلِتَجْرِىَ ٱلْفُلْكُ بِأَمْرِهِۦ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَ ﴿٤٦﴾ وَلَقَدْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ رُسُلًا إِلَىٰ قَوْمِهِمْ فَجَآءُوهُم
بِٱلْبَيِّنَـٰتِ فَٱنتَقَمْنَا مِنَ ٱلَّذِينَ أَجْرَمُوا۟ ۖ وَكَانَ حَقًّا عَلَيْنَا نَصْرُ
ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٤٧﴾ ٱللَّهُ ٱلَّذِى يُرْسِلُ ٱلرِّيَـٰحَ فَتُثِيرُ سَحَابًا فَيَبْسُطُهُۥ
فِى ٱلسَّمَآءِ كَيْفَ يَشَآءُ وَيَجْعَلُهُۥ كِسَفًا فَتَرَى ٱلْوَدْقَ يَخْرُجُ مِنْ
خِلَـٰلِهِۦ ۖ فَإِذَآ أَصَابَ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦٓ إِذَا هُمْ يَسْتَبْشِرُونَ
﴿٤٨﴾ وَإِن كَانُوا۟ مِن قَبْلِ أَن يُنَزَّلَ عَلَيْهِم مِّن قَبْلِهِۦ لَمُبْلِسِينَ
﴿٤٩﴾ فَٱنظُرْ إِلَىٰٓ ءَاثَـٰرِ رَحْمَتِ ٱللَّهِ كَيْفَ يُحْىِ ٱلْأَرْضَ بَعْدَ مَوْتِهَآ ۚ
إِنَّ ذَٰلِكَ لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٥٠﴾



**(42) Ya kai wannnan Annabi (S.A.W) ka gaya wa waxannan mushrikai, ku yi tafiya a bayan qasa, ku lura yaya qarshen al'ummun da suka qaryata gabaninku ya kasance?. lallai qarshensu ya yi muni, don mafi yawansu sun kasance mushirikai da Allah, sai aka halakar da su saboda shirkar su.**

**(43) Ya kai wannan Annabi (S.A.W) ka tsayar da fuskar ka ga addinin musulunci miqaqqe, wanda babu wata karkata a cikinsa, tun gabanin ranar alqiyama bata zo ba, ranar da idan ta zo babu mai mayar da ita. A wannan ranar mutane zasu rabu zuwa, 'yan Aljanna, ma'abota ni'ima, da kuma 'yan wuta ma'abota azaba.**

**(44) Duk wanda ya kafirce wa Allah, to cutarwar kafircin wadda ita ce dauwama a cikin wuta, kansa zata dawo, kuma duk wanda ya yi aiki nagari, yana mai neman yardar Allah, to kawunansu suka yi wa, za a shirya musu shiga Aljannah da jin daxi da abin da yake cikinta, suna masu dauwama a cikinta har abada.**

**(45) Don Allah ya sakawa waxanda suka yi imani da shi, kuma suka yi ayyuka nagari, waxanda Ubangijinsu ya yarda da su. Haqiqa Allah mai tsarki baya son masu kafirce masa, shi da Manzannin sa, kuma lallai yana qin su qi mai tsanani, zai azbtar da su ranar tashin alqiyama.**

**(46) Yana daga cikin ayoyinsa masu girma, da suke tabbatar da ikonsa, da kaxaitakarsa, yana turo da iska, tana yi wa bayi bushara da saukar ruwan sama, kuma domin ya xanxana muku rahamarsa ya ku mutane, da abin da zai faru bayan ruwan ya sauka, na kyan yanayi da arziki, kuma don jiragen ruwa su gudana cikin teku da izininsa, kuma don ku nema daga falalarsa ta hanyar kasuwanci a teku, kuma ko kwa godewa ni'imar da Allah ya yi muku, sai ya qara muku.**

**(47) Ya kai wannan Manzo, haqiqa mun aiko Annabawa gabaninka zuwa ga al'umar su, sai suka zo musu da hujjoji da dalilai, da suke nuna gaskiyar su, amma sai al'umarsu suka qaryata abin da Manzanninsu suka zo musu da shi, sai muka kama waxanda suka aikata munanan ayyuka, muka halakar da su da azabarmu, muka tseratar da Manzannin da Muminai daga halaka, lallai tseratar Manzanni da Muminai haqqi ne da muka wajabtawa kanmu.**

**(48) Allah ne yake koro iska, yake tasar da ita, sai wannan iskar ta motsa hadari, ta juya shi, sai Allah ya jera shi a cikin sama, yadda ya ga dama, da yawa ko kaxan, ya mayar da shi yanki-yanki. sai ka ga ruwa yana fita ta tsakaninsa. Idan ruwan ya samu waxanda ya ga dama daga cikin bayinsa, sai ka ga suna farin ciki da rahamar Allah a gare su, ta saukar da ruwan sama, da fitowar tsirrai a bayan qasa wanda yake biyo saukar ruwan, tsirran suna fitowa da abin da suke buqata, su da dabbobinsu.**

**(49) Haqiqa sun kasance gabanin a saukar musu da ruwan har sun debe qauna daga saukar sa.**

**(50) Ya kai wannan Annabi, ka yi duba zuwa ga alamomin ruwan sama, wanda Allah yake saukar da shi don rahama ga bayinsa, ka kalli yaya Allah yake raya qasa da abin da yake fitarwa a kanta na tsirrai kala-kala, bayan ta bushewarta. Haqiqa wanda ya raya wannan qasa busasshiya shi ne mai tashin matattu a raye, kuma shi mai iko ne a kan dukkan komai, babu abin da yake gagararsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Aiko iska, da saukar da ruwan sama, da gudanar jiragen ruwa a cikin teku, ni'imomi ne da ya wajaba mu godewa Allah a kansu.**

**2 - Halakar da masu laifi, da kuvutar da Muminai sunna ce ta Allah.**

**3 - Tsurowar qasa bayan ta bushe, dalili ne da yake tabbatar da yiwuwar tashi bayan mutuwa.**

وَلَئِنۡ أَرۡسَلۡنَا رِيحٗا فَرَأَوۡهُ مُصۡفَرّٗا لَّظَلُّواْ مِنۢ بَعۡدِهِۦ يَكۡفُرُونَ
٥١ فَإِنَّكَ لَا تُسۡمِعُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَلَا تُسۡمِعُ ٱلصُّمَّ ٱلدُّعَآءَ إِذَا وَلَّوۡاْ
مُدۡبِرِينَ ٥٢ وَمَآ أَنتَ بِهَٰدِ ٱلۡعُمۡيِ عَن ضَلَٰلَتِهِمۡۖ إِن تُسۡمِعُ إِلَّا
مَن يُؤۡمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُم مُّسۡلِمُونَ ٥٣ ۞ ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَكُم
مِّن ضَعۡفٖ ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعۡدِ ضَعۡفٖ قُوَّةٗ ثُمَّ جَعَلَ مِنۢ بَعۡدِ
قُوَّةٖ ضَعۡفٗا وَشَيۡبَةٗۚ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ وَهُوَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡقَدِيرُ
٥٤ وَيَوۡمَ تَقُومُ ٱلسَّاعَةُ يُقۡسِمُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ مَا لَبِثُواْ غَيۡرَ
سَاعَةٖۚ كَذَٰلِكَ كَانُواْ يُؤۡفَكُونَ ٥٥ وَقَالَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلۡعِلۡمَ وَٱلۡإِيمَٰنَ لَقَدۡ لَبِثۡتُمۡ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡبَعۡثِۖ
فَهَٰذَا يَوۡمُ ٱلۡبَعۡثِ وَلَٰكِنَّكُمۡ كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ ٥٦ فَيَوۡمَئِذٖ
لَّا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مَعۡذِرَتُهُمۡ وَلَا هُمۡ يُسۡتَعۡتَبُونَ
٥٧ وَلَقَدۡ ضَرَبۡنَا لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٖۚ
وَلَئِن جِئۡتَهُم بِـَٔايَةٖ لَّيَقُولَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِنۡ أَنتُمۡ إِلَّا
مُبۡطِلُونَ ٥٨ كَذَٰلِكَ يَطۡبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ
٥٩ فَٱصۡبِرۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞۖ وَلَا يَسۡتَخِفَّنَّكَ ٱلَّذِينَ لَا يُوقِنُونَ ٦٠

ثلاثة أرباع الحزب ٤١



**51 Kuma idan muka aiko da iska ta lalata tsirransu da shuke-shukensu, sai ka ga shuke-shukensu sun yi fatsi-fatsi, bayan ta kasance koriya shar, da za su ga haka, da sun ci gaba da kafirce wa ni'imomin Allah, waxanda suka gabata, duk da yawansu.**

**52 Kamar yadda ba zaka iya jiyar da mamata ba, haka ma ba zaka iya jiyar da kurame ba, don duk sun yi maka nisa, to haka ma baza ka iya shiryar da waxanda suka yi kama da su ba, ta wajen bijirewa da rashin amfanuwa da abin da ka zo a shi.**

**53 Kai ba mai iya datar da wanda ya vace daga tafarki madaidaici ba ne zuwa ga haryar shiriya. Haka ma baka jiyarwa, jin da zai yi amfani sai ga wanda ya yi imani da ayoyinmu, domin shi ne yake amfanuwa da abin da kake faxa, kuma su masu jayuwa ne ga lamarinmu, masu qasqantar da kai ne.**

**54 Allah shi ne ya halicce ku – Ya ku mutane - daga wulaqantaccen ruwa, sannan ya sanya muku qarfin mutuntaka, bayan raunin yarinta, sannan ya sanya muku raunin girma, da tsufa, bayan qarfin mutuntaka. Allah yana halittar abin da ya ga dama na qarfi, da rauni, shi ne masanin dukkan komai, mai ikon da babu wani abin da yake gajiyar da shi.**

**55 Ranar da alqiyama zata tsaya, masu laifi za su rantse cewa, basu zauna a cikin qabarinsu ba sai xan wani lokaci kaxan. To kamar yadda aka kautar da su ga barin sanin gwargwadon zamansu a qabari, haka aka kautar da su ga barin bin gaskiya a nan duniya.**

**56 Waxanda Allah ya ba wa ilimi cikin Annabawa da Mala'iku suka ce: "Ai kun zauna ne gwargwadon abin da Allah ya rubuta muku, tun daga ranar halittarku har zuwa ranar da za a tashe ku, ranar da kuka yi inkarin zuwanta, sai dai ku baku san tashi bayan mutuwa sai ya faru ba, don haka kuka kafirce masa.**

**57 Ranar da Allah zai tashi duk halitta, don yi musu sakayya da hisabi, abin da azzalumai suka qirqira na uzuri ba zai amfane su ba, kuma ba za a nemi su yi abin da Allah zai yarda da su ba, na tuba da komawa zuwa gare shi, don lokacin hakan ya wuce.**

**58 Haqiqa mun bugawa mutane dukkanin wani misali a cikin wannan Alqur'ani, saboda kulawar mu da su, domin gaskiya ta bayyana a gare su daga vata. Ya kai wannan Annabi (S. A.W) da zaka zo musu da wata hujja a kan gaskiyarka, to da waxanda suka kafircewa Allah sun ce: "Lallai ku masu varna ne cikin abin da kuka zo da shi".**

**59 Kamar yadda aka rufe zukatan waxannan mutane, ko ka zo musu da aya baza su yi imani da ita ba, haka Allah yake rufe zukatan duk waxanda basu san abin da ka zo da shi gaskiya ne.**

**60 Ka yi haquri ya kai wannan Manzo, game da qaryata ka da mutanen ka suka yi. Tabbas alqawarin da Allah ya yi maka na taimako, da tabbatuwa a bayan qasa, yana nan babu makawa. Kada waxanda basu yarda za a tashe su ba, su ingizaka ka yi gaggawa, ko ka bar haquri.**

## Kaxan Daga Abin Da Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yadda kafirai suke xebe qauna daga rahamar Allah, yayin da bala'i ya sauka.**
**2 - Datarwa ga shiriya a hannun Allah take. Ba a hannun Manzon Allah (S.A.W) ba.**
**3 - Matakan rayuwa izina ce ga masu wa'azantuwa.**
**4 - Taruwar zunubai suke kawo rufewar zuciya.**

سُورَةُ لُقْمَان
آيَاتُهَا ٣٤ ترتيبها ٣١

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ١ تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْحَكِيمِ ٢ هُدًى وَرَحْمَةً
لِّلْمُحْسِنِينَ ٣ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤْتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُم
بِٱلْءَاخِرَةِ هُمْ يُوقِنُونَ ٤ أُو۟لَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدًى مِّن رَّبِّهِمْ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ٥ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشْتَرِى لَهْوَ ٱلْحَدِيثِ
لِيُضِلَّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ بِغَيْرِ عِلْمٍ وَيَتَّخِذَهَا هُزُوًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمْ
عَذَابٌ مُّهِينٌ ٦ وَإِذَا تُتْلَىٰ عَلَيْهِ ءَايَٰتُنَا وَلَّىٰ مُسْتَكْبِرًا
كَأَن لَّمْ يَسْمَعْهَا كَأَنَّ فِىٓ أُذُنَيْهِ وَقْرًا ۖ فَبَشِّرْهُ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٧
إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمْ جَنَّٰتُ ٱلنَّعِيمِ ٨
خَٰلِدِينَ فِيهَا ۖ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقًّا ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ٩ خَلَقَ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيْرِ عَمَدٍ تَرَوْنَهَا ۖ وَأَلْقَىٰ فِى ٱلْأَرْضِ رَوَٰسِىَ أَن تَمِيدَ
بِكُمْ وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَآبَّةٍ ۚ وَأَنزَلْنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَنۢبَتْنَا
فِيهَا مِن كُلِّ زَوْجٍ كَرِيمٍ ١٠ هَٰذَا خَلْقُ ٱللَّهِ فَأَرُونِى مَاذَا
خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ بَلِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ١١



# Suratu Luqmaan

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayyana hikimar da (Allah ya ba wani) wadda ta dace da shari'a, da Ambaton Luqman misali a kan haka:**

## Tafsir:

**1 (Alif, Laam, Meem). Bayanin ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon Suratul Baqara.**

**2 Waxannan ayoyi da aka saukar maka - Ya kai wannan Manzo - ayoyi ne na littafi da yake magana cikin hikima.**

**3 Kuma shiriya ne, da jin qai, ga waxanda suke kyautata ayyukansu, ta hanyar tsayuwa da haqqoqin Ubangijinsu, da haqqoqin bayinsa.**

**4 Waxanda suke yin salla a cikin mafi cikar sifa, kuma suke bayar da zakkar dukiyoyin su, suna masu sakankancewa da abin da yake a lahira, na tashi bayan mutuwa, da hisabi, da lada, da uquba.**

**5 Waxancan masu siffatuwa da waxancan siffofin da aka ambata, suna kan shiriya daga Ubangijinsu, kuma su ne masu rabauta, da samun abin da suke nema, da nisanta da abin da suke jin tsoro.**

**Yayin da Allah ya ambaci siffofin masu kyautatawa, sai kuma ya ambaci siffofin masu munanawa, ya ce:**

**6 Akwai daga cikin mutane, kamar - Nadir bin Haris - waxanda suke zavar zantuka masu shagaltarwa, domin su kawar da mutane da waxannan zantuka daga addinin Allah, ba tare da ilimi ba, kuma suke riqi ayoyin Allah ababen izgili, suna izgili da su. Masu waxannan siffofi suna da azabar qasqanci a lahira.**

**7 Idan ana karanta masa ayoyinmu sai ka ga ya bada baya, yana mai girman kai daga jin su, kamar bai ji su ba, kamar a cikin kunnuwansa akwai kurumta ta jin murya, ya kai wannan Manzo ka yi masa bushara da azaba mai raxaxi, da take jiran sa.**

**8 Lallai waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki nagari, Aljannatai na ni'ima sun tabbata a gare su, zasu yi ta shan daxi da abin da Allah ya tanadar musu a cikinta.**

**9 Zasu yita rayuwa a ciki. Allah yayi musu alqawarin dawwama, domin Allah shine mai qarfin da babu wanda ya isa ya rinjaye shi, kuma shine mai tarin hikima, a cikin halittar sa, gudanarwar sa, shari'ar sa.**

**10 Allah ya halicci sammai xaukaka, ba tare da ginshiqi ba, ya kafa duwatsu tabbatattu a bayan qasa, don kada ta motsa da ku, ya yaxa dabbobi kala-kala a bayan qasa. Mun saukar da ruwan sama daga sama, muka fitar da kowane irin kala mai kyan gani daga tsirrai, waxanda mutane da dabbobi suke amfani da su.**

**11 Duk abubuwan da aka ambata, halittar Allah ne. Ya ku mushirikai mene ne allolinku suka halitta? Tabbas azzalumai suna cikin vata daga gaskiya bayyananne, ta yadda suke shirka da Ubangijinsu, da abubuwan da basa iya halittar komai, su ake halitta.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Biyayya ga Allah tana kaiwa ga rabauta, a duniya da lahira.**

**2 - Haramta duk abin da zai hana tabbatar da tafarkin Allah, na Magana, ko aiki.**

**3 - Girman kai yana hana karvar gaskiya.**

**4 - Allah ne kaxai ya kevanta da yin halitta, kuma ya qalubalanci kafirai a kan allolinsu su halicci wani abu in zasu iya.**

وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا لُقْمَٰنَ ٱلْحِكْمَةَ أَنِ ٱشْكُرْ لِلَّهِ ۚ وَمَن يَشْكُرْ فَإِنَّمَا
يَشْكُرُ لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ حَمِيدٌ ١٢ وَإِذْ قَالَ
لُقْمَٰنُ لِٱبْنِهِۦ وَهُوَ يَعِظُهُۥ يَٰبُنَىَّ لَا تُشْرِكْ بِٱللَّهِ ۖ إِنَّ ٱلشِّرْكَ
لَظُلْمٌ عَظِيمٌ ١٣ وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حَمَلَتْهُ أُمُّهُۥ
وَهْنًا عَلَىٰ وَهْنٍ وَفِصَٰلُهُۥ فِى عَامَيْنِ أَنِ ٱشْكُرْ لِى وَلِوَٰلِدَيْكَ
إِلَىَّ ٱلْمَصِيرُ ١٤ وَإِن جَٰهَدَاكَ عَلَىٰٓ أَن تُشْرِكَ بِى مَا لَيْسَ
لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ فَلَا تُطِعْهُمَا ۖ وَصَاحِبْهُمَا فِى ٱلدُّنْيَا مَعْرُوفًا ۖ
وَٱتَّبِعْ سَبِيلَ مَنْ أَنَابَ إِلَىَّ ۚ ثُمَّ إِلَىَّ مَرْجِعُكُمْ فَأُنَبِّئُكُم
بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ١٥ يَٰبُنَىَّ إِنَّهَآ إِن تَكُ مِثْقَالَ حَبَّةٍ مِّنْ
خَرْدَلٍ فَتَكُن فِى صَخْرَةٍ أَوْ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ أَوْ فِى ٱلْأَرْضِ يَأْتِ
بِهَا ٱللَّهُ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَطِيفٌ خَبِيرٌ ١٦ يَٰبُنَىَّ أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ وَأْمُرْ
بِٱلْمَعْرُوفِ وَٱنْهَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَٱصْبِرْ عَلَىٰ مَآ أَصَابَكَ ۖ إِنَّ ذَٰلِكَ
مِنْ عَزْمِ ٱلْأُمُورِ ١٧ وَلَا تُصَعِّرْ خَدَّكَ لِلنَّاسِ وَلَا تَمْشِ فِى ٱلْأَرْضِ
مَرَحًا ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ ١٨ وَٱقْصِدْ فِى مَشْيِكَ
وَٱغْضُضْ مِن صَوْتِكَ ۚ إِنَّ أَنكَرَ ٱلْأَصْوَٰتِ لَصَوْتُ ٱلْحَمِيرِ ١٩



**(12) Haqiqa mun ba wa Luqman fahimtar addini, da dacewa ga daidai, cikin al'amura, muka ce masa: Ya kai Luqman ka godewa Ubangijinka saboda ni'imar da ya yi maka da dacewa da yi masa xa'a, duk wanda ya godewa Ubangijinsa, to amfanin godiyar kansa zai dawo, domin Allah Mawadaci ne ga godiyarsa, kuma duk wanda ya butulcewa ni'imar Allah, ya kafirce masa, to illar Kafircinsa a kansa zata koma, ba zai cuci Allah da komai ba, domin shi Mawadaci ne ga barin bayinsa gaba xaya, kuma abin godiya ne a kowane hali.**

**(13) Ka ambata - Ya kai wannan Manzo - lokacin da Luqmaan ya cewa xansa, yana mai kwadaitar da shi a kan alheri, yana mai tsoratar da shi daga sharri, ya ce masa: "Ya kai xana kada ka bautawa wani tare da Allah, lallai bautawa wani tare da Allah zalunci ne mai girma, mutum ya yi wa kansa, don ya aikata laifi mafi girma da yake dauwamar da mutum a cikin wuta".**

**(14) Mun yi wa mutun wasiyya da biyayya ga iyayensa, da yi musu xa'a cikin abin da bai savawa Allah ba. Mahaifiyar sa ta xauke shi a cikinta, wahala a kan wahala, a daina shayar da shi bayan shekara biyu. Muka ce masa: "Ka godewa Allah ni'imar da ya yi maka, sannan ka godewa iyayen ka, saboda wahalar da suka sha ta rainon ka, da kulawa da kai, gare ni kaxai za a koma, in sakawa kowa da abin da ya cancance shi.**

**(15) Idan iyaye suka yi qoqarin su sa ka yi shirka da Allah, da qarfi, to kada ka yi musu xa'a akan haka, domin babu biyayya ga wani abin halitta a cikin savawa Mahalicci. Kuma ka zauna lafiya da su, a wannan duniya, ta hanyar kyautata musu, da sada zumunci, kuma ka bi hanyar wanda ya koma zuwa gare ni, da hanyar kaxaita Allah, da yi masa biyayya. Sannan gare ni kaxai makomarku take ranar alqiyama, sai in baku labarin abubuwan da kuka kasance kuna aikatawa a duniya, in saka muku a kansu.**

**(16) Ya kai xana, mummunan aiki, ko kyakkyawa, komai qanqantar su, koda a cikin dutse suke, ko a wani wuri, a sama, ko qasa, inda babu mai ganin su, to Allah zai zo da su a ranar alqiyama, sai ya sakawa bawa a kansu. Haqiqa Allah mai tausasawa ne, qananan abubuwa basa vuya a gare shi, masani ne dangane da inda suke.**

**(17) Ya kai xana, ka tsayar da sallah, a cikin siffa mafi cika, ka yi umarni da kyakkyawa, ka yi hani ga mummuna, kuma ka yi haquri da abin da zai same ka a kan haka. Wannan abin da aka umarce ka da shi, yana daga cikin abin da Allah ya xora maka ka aikata, baka da wani zavi a kan haka.**

**(18) Kada ka kawar da fuskarka ga mutane saboda girman kai, kada ka yi tafiya a bayan qasa kana mai fariya, da ji da kai. Haqiqa Allah baya son duk wani mai taqama a tafiyarsa, mai alfahari da ni'imar da Allah ya ba shi, yana yi wa mutane girman kai da ita, kuma baya gode Allah a kanta.**

**(19) Ka zama tsaka-tsaki cikin tafiyarka, tsakanin sauri da tafiya a hankali, kana mai bayyana nutsuwa, kuma ka sassauta muryarka, kada ka xaga ta xagawar da zata cutar, lallai mafi munin murya ita ce muryar jakai, saboda yadda suke xaga muryoyinsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yayin da Allah ya yi bayanin abin da yake samun uwa na wahalar ciki da haihuwa, sai hakan ya nuna qarin yi mata biyayya.**

**2 - Amfanin xa'a ga Allah da cutarwar da take cikin savo, duk suna komawa zuwa ga bawa..**

**3 - Wajabcin kulawa da ilimi, da tarbiyyar 'ya'ya.**

**4 - Ladubba a musulunci sun haxa da ladubban xaixakun mutane da jama'a.**

أَلَمْ تَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَأَسْبَغَ
عَلَيْكُمْ نِعَمَهُۥ ظَٰهِرَةً وَبَاطِنَةً ۗ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِى ٱللَّهِ
بِغَيْرِ عِلْمٍ وَلَا هُدًى وَلَا كِتَٰبٍ مُّنِيرٍ ﴿٢٠﴾ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱتَّبِعُوا۟
مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُوا۟ بَلْ نَتَّبِعُ مَا وَجَدْنَا عَلَيْهِ ءَابَآءَنَآ ۚ أَوَلَوْ كَانَ
ٱلشَّيْطَٰنُ يَدْعُوهُمْ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلسَّعِيرِ ﴿٢١﴾ ۞ وَمَن يُسْلِمْ الحِزْبُ ٤٢
وَجْهَهُۥٓ إِلَى ٱللَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ ۗ
وَإِلَى ٱللَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلْأُمُورِ ﴿٢٢﴾ وَمَن كَفَرَ فَلَا يَحْزُنكَ كُفْرُهُۥٓ ۚ
إِلَيْنَا مَرْجِعُهُمْ فَنُنَبِّئُهُم بِمَا عَمِلُوٓا۟ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ
﴿٢٣﴾ نُمَتِّعُهُمْ قَلِيلًا ثُمَّ نَضْطَرُّهُمْ إِلَىٰ عَذَابٍ غَلِيظٍ ﴿٢٤﴾
وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ ٱللَّهُ ۚ قُلِ
ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٢٥﴾ لِلَّهِ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ ﴿٢٦﴾ وَلَوْ أَنَّمَا فِى ٱلْأَرْضِ
مِن شَجَرَةٍ أَقْلَٰمٌ وَٱلْبَحْرُ يَمُدُّهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ سَبْعَةُ أَبْحُرٍ
مَّا نَفِدَتْ كَلِمَٰتُ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ﴿٢٧﴾ مَّا خَلْقُكُمْ
وَلَا بَعْثُكُمْ إِلَّا كَنَفْسٍ وَٰحِدَةٍ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ ﴿٢٨﴾



**(20) Ya ku mutane, shin baku ga yadda Allah ya sauwaqe muku amfanuwa da abin da yake cikin sammai ba, daga rana, da wata, da taurari, kuma ya sauwaqe muku abin da yake cikin qassai, kamar dabbobi, da bishiyoyi, da tsirrai, Kuma Allah ya cika muku ni'imominsa bayyanannu, waxanda ake gani, kamar kyan sura,da kyakkyawar kama, na ni'imomi voyayyu, kamar hankali, da ilimi, Amma duk da waxannan ni'imomi, daga cikin mutane akwai wanda yake jayayya da kaxaitar Allah, ba tare da wani ilimi ba, wanda ya dogara a kan wahayi daga Allah, ko wani hankali mai haske, ko wani littafi bayyanan ne da Allah ya saukar.**

**(21) Idan aka ce wa waxannan masu jayayya da kaxaitakar Allah, "Ku bi abin da Allah ya saukarwa Manzonsa na wahayi", sai su ce ba zamu bi ba, muna bin abin da muka samu magabatanmu a kai ne, na bautawa allolinmu. Shin sun yarda su yi wa magabatan su biyayya koda kuwa shaixan ne yake kiran su, zuwa ga azabar Sa'ira ranar alqiyama.**

**(22) Duk wanda ya fuskanci Allah, yana mai tsarkake bauta a gare shi, mai kyautata aikinsa, to haqiqa ya yi riqo da mafi tabbacin abin da wanda yake son tsira yake yin riqo da shi, ba a tsoron yankewar sa, lallai ga Allah kaxai makomar al'amura take, kuma zai sakawa kowa da abin da ya cancance shi.**

**(23) Duk wanda ya kfircewa Allah, to kada kafircinsa ya baqanta maka rai – Ya kai wannan Manzo – gare mu makomarsu kaxai take ranar alqiyama, sai mu basu labarin munanan abubuwan da suka aikata a duniya, mu saka musu a kansu, Haqiqa Allah Masanin abin da yake cikin qiraza ne, babu abin da yake vuya a gare shi daga cikinsu.**

**(24) Zamu jiyar dasu daxi, xan qanqani, a wannan Duniya, ta hanyar abubuwan more rayuwa, sannan ranar alqiyama, mu komar da su ga azaba mai tsanani, ita ce azabar wuta.**

**(25) Ya kai wannan Manzo idan ka tambayi waxannan mushirikai cewa: "Waye ya halicci sammai, kuma ya halicci qassai? Tabbas za su ce maka: "Allah ne ya halicce su" to ka ce da su: "Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya bayyana hujja a kanku, sai dai da yawa daga cikinsu ba su san wanda ya cancanci godiya ba, saboda jahilcinsu.**

**(26) Duk abin da yake cikin sammai da qassai, na Allah ne, shi ya halicce su, ya mallake su, yake gudanar da su. Haqiqa Allah shi ne mawadaci daga dukkan abubuwan da ya halitta, kuma abin godewa a duniya da lahira.**

**(27) Da a ce, duk abin da yake bayan qasa na bishiyoyi, za a fiqe su, su zama alqalami, kuma a sanya teku ya zama tawwada gare su, koda an qara su sun zama guda bakwai, to da kalmomin Allah baza su qare ba, don basu da iyaka. Haqiqa Allah Mabuwayi ne, babu wanda yake iya galaba a kansa, kuma mai hikima ne a cikin halittarsa da tsarinsa.**

**(28) Halittarku – Ya ku mutane – da tashinku ranar alqiyama don yi muku hisabi da sakamako, ba komai ba ce face kamar halittar rai guda xaya da tashinta ne bayan mutuwa, wajen sauqi. Haqiqa Allah jin wani sauti baya hana jin wani sautin, kuma mai gani ne, wani ganin baya shagaltar da shi daga ganin wani abu, to haka nan ma halittar wata rai da tashin ta bayan mutuwa baya shagaltarwa daga halittar wata ran da tashin ta ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sanin ni'imomin Allah hanyace ta yi masa godiya, da kuma yin imani da shi, ba wai hanya ce ta kafirce masa ba.**

**2 - Haxarin makauniyar biyayya, Musamman a al'amura na aqida.**

**3 - Muhimmancin miqa wuya ga Allah, da jawuwa gare shi, da kyautata aiki, don samun yardar Allah.**

**4 - Kalmomin Allah basa qarewa.**

أَلَمْ تَرَ أَنَّ ٱللَّهَ يُولِجُ ٱلَّيْلَ فِى ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِى ٱلَّيْلِ
وَسَخَّرَ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ كُلٌّ يَجْرِىٓ إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى وَأَنَّ ٱللَّهَ
بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ٢٩ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْحَقُّ وَأَنَّ مَا يَدْعُونَ
مِن دُونِهِ ٱلْبَٰطِلُ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْكَبِيرُ ٣٠ أَلَمْ تَرَ أَنَّ
ٱلْفُلْكَ تَجْرِى فِى ٱلْبَحْرِ بِنِعْمَتِ ٱللَّهِ لِيُرِيَكُم مِّنْ ءَايَٰتِهِۦٓ إِنَّ
فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّكُلِّ صَبَّارٍ شَكُورٍ ٣١ وَإِذَا غَشِيَهُم مَّوْجٌ
كَٱلظُّلَلِ دَعَوُا۟ ٱللَّهَ مُخْلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ فَلَمَّا نَجَّىٰهُمْ إِلَى ٱلْبَرِّ
فَمِنْهُم مُّقْتَصِدٌ وَمَا يَجْحَدُ بِـَٔايَٰتِنَآ إِلَّا كُلُّ خَتَّارٍ كَفُورٍ
٣٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُوا۟ رَبَّكُمْ وَٱخْشَوْا۟ يَوْمًا لَّا يَجْزِى وَالِدٌ
عَن وَلَدِهِۦ وَلَا مَوْلُودٌ هُوَ جَازٍ عَن وَالِدِهِۦ شَيْـًٔا إِنَّ وَعْدَ ٱللَّهِ
حَقٌّ فَلَا تَغُرَّنَّكُمُ ٱلْحَيَوٰةُ ٱلدُّنْيَا وَلَا يَغُرَّنَّكُم بِٱللَّهِ
ٱلْغَرُورُ ٣٣ إِنَّ ٱللَّهَ عِندَهُۥ عِلْمُ ٱلسَّاعَةِ وَيُنَزِّلُ ٱلْغَيْثَ
وَيَعْلَمُ مَا فِى ٱلْأَرْحَامِ وَمَا تَدْرِى نَفْسٌ مَّاذَا تَكْسِبُ غَدًا
وَمَا تَدْرِى نَفْسٌۢ بِأَىِّ أَرْضٍ تَمُوتُ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٌۢ ٣٤

آيَاتُهَا ٣٠ سُورَةُ ٱلسَّجْدَةِ تَرْتِيبُهَا ٣٢



29 **Ashe baka ga yadda Allah yake rage dare ba, don ya qara yini, kuma ya rage yini don ya qara dare, kuma ya qaddara matafiyar rana da wata, kowannen su yana tafiya a cikin matafiyarsa zuwa wani lokaci qayyadadde. Haqiqa Allah dangane da abin da kuke aikatawa masani ne mai bada labari, babu abin da yake vuya daga gare shi, na daga ayyukanku, kuma zai saka muka a kansu.**

30 **Wannan gudanarwa, da tsarawa, suna tabbatar da cewa: Allah shi kaxai ne gaskiya, shi gaskiya ne a zatin sa, da siffofinsa, da ayyukansa, kuma abubuwan da mushrikai suke bautawa koma bayan Allah, duk vata ne maras tushe, kuma haqiqa Allah shi ne maxaukaki da zatinsa, da rijayensa, da tsarinsa a kan dukkan halittarsa, wanda babu maxaukaki sama da shi, wanda shi ya fi komai girma.**

31 **Ashe baka ga yadda jiragen ruwa suke tafiya a kan teku ba, cikin tausasawar Allah da horewarsa, don ya nuna muku – Ya ku mutane – kaxan daga ayoyin sa da suke nuna ikonsa da tausasawarsa. Haqiqa a cikin wannan akwai dalilai a kan ikon Allah, (Abin lura) ga duk wani mai yawan haquri a kan abin da yake samunsa na cuta, mai yawan godewa Allah a kan abin da yake samunsa na ni'ima.**

32 **Idan kumfar teku ta kewaye su ta kowane vangare, kai ka ce duwatsu ne, ko wani girgije mai girma, sai su kira Allah shi kaxai, suna masu tsarkake shi da addua da bauta. Yayin da Allah ya amsa musu addu'arsu, ya tseratar da su zuwa tudu, ya kuvutar da su daga nutsewa, sai ka ga a cikinsu akwai wanda yake tsaka-tsaki, bai yi abin da aka wajabta masa ba, na godiya, kamar yadda ya kamata. A cikinsu kuma akwai wanda yake qaryata ni'imar Allah. Babu wanda yake jayayya da ayoyinmu sai wanda yake mayaudari, kamar wannan da ya yi wa Allah alqawari cewa idan ya tseratar da shi zai kasance cikin masu godewa Allah, sannan mai yawan butulcewa ni'imomin Ubangijinsa waxanda ya yi masa ni'ima da su.**

33 **Ya ku mutane, ku ji tsoron Ubangijinku, ta hanyar aikata umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, ku ji tsoron azabar ranar da mahaifi ba zai amfanawa abin da ya haifa da komai ba, haka shi ma xan ba zai amfanawa mahaifinsa da komai ba, lallai alqawarin Allah na sakayya gaskiya ne, kuma mai faruwa ne ba makawa, don haka kada rayuwar duniya ta yaudare ku, da abubuwan da su ke cikinta na sha'awace sha'awace, da kuma abubuwa masu shagaltarwa, kuma kada shaixan ya yaudare ku da haqurin Allah da jinkirta azaba a kanku.**

34 **Haqiqa a wurin Allah ne kaxai sanin ranar da alqiyama zata tsaya yake, kuma shi ne yake saukar da ruwan sama, lokacin da ya ga dama, kuma shi ne kaxai ya san abin da yake cikin mahaifa, namiji ne, ko mace, xan-wuta ne, ko xan-Aljannah ne, kuma babu wata rai da ta san mai zai same ta gobe, na alheri, ko sharri, kuma babu wata rai da ta san a inda zata mutu, Allah shi kaxai ne ya san duk abin da ya gabata, haqiqa Allah Masani ne, kuma mai bada labari, babu abin da yake vuya a gare shi daga cikinsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tauye dare da rana, ko qara kowanne daga cikinsu, da kuma hore rana da da wata, duk ayoyi ne da suke tabbatar da ikon Allah Maxaukakin sarki, kuma ni'imomi ne da suka cancanci godiya.**

**2 - Haquri da godiya, hanyoyi ne guda biyu na yin izina da ayoyin Allah.**

**3 - Tsoron tashin alqiyama yana hana ruxuwa da duniya, da biyewa ruxin Shaixan**

**4 - Ilimin Allah ya game dukkan gaibu.**

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ١ تَنزِيلُ ٱلۡكِتَٰبِ لَا رَيۡبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ
٢ أَمۡ يَقُولُونَ ٱفۡتَرَىٰهُۚ بَلۡ هُوَ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوۡمٗا
مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٖ مِّن قَبۡلِكَ لَعَلَّهُمۡ يَهۡتَدُونَ ٣ ٱللَّهُ
ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ
ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ مَا لَكُم مِّن دُونِهِۦ مِن وَلِيّٖ وَلَا شَفِيعٍۚ
أَفَلَا تَتَذَكَّرُونَ ٤ يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ يَعۡرُجُ
إِلَيۡهِ فِي يَوۡمٖ كَانَ مِقۡدَارُهُۥٓ أَلۡفَ سَنَةٖ مِّمَّا تَعُدُّونَ ٥ ذَٰلِكَ
عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ٦ ٱلَّذِيٓ أَحۡسَنَ
كُلَّ شَيۡءٍ خَلَقَهُۥۖ وَبَدَأَ خَلۡقَ ٱلۡإِنسَٰنِ مِن طِينٖ ٧ ثُمَّ جَعَلَ
نَسۡلَهُۥ مِن سُلَٰلَةٖ مِّن مَّآءٖ مَّهِينٖ ٨ ثُمَّ سَوَّىٰهُ وَنَفَخَ فِيهِ مِن
رُّوحِهِۦۖ وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَۚ قَلِيلٗا
مَّا تَشۡكُرُونَ ٩ وَقَالُوٓاْ أَءِذَا ضَلَلۡنَا فِي ٱلۡأَرۡضِ أَءِنَّا لَفِي
ربع الحزب ٤٢ خَلۡقٖ جَدِيدِۭۚ بَلۡ هُم بِلِقَآءِ رَبِّهِمۡ كَٰفِرُونَ ١٠ ۞ قُلۡ يَتَوَفَّىٰكُم
مَّلَكُ ٱلۡمَوۡتِ ٱلَّذِي وُكِّلَ بِكُمۡ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ تُرۡجَعُونَ ١١



# Suratus Sajda

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin hujjojin gaskiya, da abubuwan da ake gani, waxanda Alqur'ani ya sauka da su. Daga cikinsu akwai bayanin haqiqanin halitta da halayen da mutum yake cikinsu.**

## Tafsir:

**(1) (Alif, Laam, Meem).Bayani ya gabata a kan ire-iren waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara.**

**(2) Wannan Alqur'ani da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi, saukakke ne daga Ubangijin talikai, babu shakka a cikinsa.**

**(3) Waxannan kafiran suna cewa: "Muhammad ya qirqiri wannan Alqur'ani ga Ubangijinsa" lamarin ba haka ba ne, shi Alqur'ani gaskiya ne da babu kokwanto a cikinsa, abin saukarwa ne daga Ubangijinka - Ya kai wannan Manzo - domin ka tsoratar da mutanen da Manzo bai zo musu ba gabaninka da azabar Allah, ko sa shiriya ga gaskiya, su bi ta, su yi aiki da ita.**

**(4) Allah ne ya halicci Sammai, kuma ya halicci qassai, kuma ya halicci abin da yake tsakaninsu a kwanaki shida, amma shi mai ikon halittarsu ne a qasa da qiftawar ido, sannan sai ya xaukaka a kan Al'arshi, xaukakar da dace da girmansa. Ya ku mutane baku da wani majivincin lamari, da zai jivinci lamarinku, ko wani mai ceto da zai cece ku a wurin Ubangijinku, ba zaku yi tunani ba?. Ku bautawa Allah wanda ya halicce ku, kada ku bautawa wani tare da shi.**

**(5) Allah yana gudanar da lamarin dukkan halittarsa, a cikin sammai da qassai, sannan wannan lamari ya xaga zuwa gareshi, a ranar da tayi dai dai da shekara dubu a lissafin ku na Duniya.**

**(6) Wannan da yake gudanar da wannan gaba xaya, shi ne masanin abin da yake nan da wanda baya nan, babu wani abu a cikinsu da yake vuya a gare shi, shi ne Mabuwayin da ba wanda yake rinjayarsa, shi ne mai xaukar fansa a kan maqiyansa, mai jin qai ga bayin sa muminai.**

**(7) Shi ne wanda ya kyautata halittar komai, kuma ya fari halittar Annabi Adam daga tavo, ba tare da ya samfuri a wurin wani ba.**

**(8) Sannan ya sanya zuriyarsa, da ta zo bayansa, daga ruwa da ya fito daga gare shi (Maniyyi).**

**(9) Sannan ya cika halittar xan Adam, ya daidaita ta, kuma ya busa masa rai, ta hanyar umartar Mala'ikan da ya wakilta, don busa rai, kuma Allah ya sanya muku – Ya ku Mutane - kunnuwa don ku riqa ji da su, ya sanya muku idanu don ku riqa gani da su, ya sanya muku zukata don ku riqa hankalta da su, amma yan kaxan ne suke yin godiya a kan waxannan ni'imomin da Allah ya yi muku ni'ima da su.**

**(10) Mushirikan da suka qaryata tashi bayan mutuwa suka ce: "Idan mun mutu, mun vace a cikin qasa, jikin mu ya koma turvaya, shin da gaske ne wai za a tashe mu a sabuwar halitta? Ai hankali ba zai xauka ba! kawai dai a haqiqanin lamarinsu masu kafircewa tashi bayan mutuwa ne, ba su yi imani da shi ba.**

**(11) Ka ce - Ya kai wannan Manzo - ga waxannan mushirikai, masu qaryata tashi bayan mutuwa cewa: "Mala'ikan mutuwa ne yake karvar ranku, wanda aka wakilta shi a kan karvar rayuka, sannan gare mu, mu kaxai zaku dawo don hisabi, da sakamako ranar alqiyama.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Hikimar turo da Manzanni, ita ce su shiryar da mutanensu ga tafarki madaidaici. 2 - Tabbatar da siffar daidaituwar Allah a kan Al'arshi, ba tare da kamantawa ko misaltawa ba. 3 - Mushirikai suna ganin rashin yiwuwar tashi bayan mutuwa, tare da cewa akwai bayyanannun hujjoji a kan hakan.**

وَلَوْ تَرَىٰٓ إِذِ ٱلْمُجْرِمُونَ نَاكِسُوا۟ رُءُوسِهِمْ عِندَ رَبِّهِمْ
رَبَّنَآ أَبْصَرْنَا وَسَمِعْنَا فَٱرْجِعْنَا نَعْمَلْ صَٰلِحًا إِنَّا مُوقِنُونَ
١٢ وَلَوْ شِئْنَا لَءَاتَيْنَا كُلَّ نَفْسٍ هُدَىٰهَا وَلَٰكِنْ حَقَّ
ٱلْقَوْلُ مِنِّى لَأَمْلَأَنَّ جَهَنَّمَ مِنَ ٱلْجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ أَجْمَعِينَ
١٣ فَذُوقُوا۟ بِمَا نَسِيتُمْ لِقَآءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَآ إِنَّا نَسِينَٰكُمْ
وَذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلْخُلْدِ بِمَا كُنتُمْ تَعْمَلُونَ ١٤ إِنَّمَا يُؤْمِنُ
بِـَٔايَٰتِنَا ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُوا۟ بِهَا خَرُّوا۟ سُجَّدًا وَسَبَّحُوا۟ بِحَمْدِ
رَبِّهِمْ وَهُمْ لَا يَسْتَكْبِرُونَ ۩ ١٥ تَتَجَافَىٰ جُنُوبُهُمْ سجدة
عَنِ ٱلْمَضَاجِعِ يَدْعُونَ رَبَّهُمْ خَوْفًا وَطَمَعًا وَمِمَّا رَزَقْنَٰهُمْ
يُنفِقُونَ ١٦ فَلَا تَعْلَمُ نَفْسٌ مَّآ أُخْفِىَ لَهُم مِّن قُرَّةِ أَعْيُنٍ
جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ١٧ أَفَمَن كَانَ مُؤْمِنًا كَمَن كَانَ فَاسِقًا
لَّا يَسْتَوُۥنَ ١٨ أَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمْ
جَنَّٰتُ ٱلْمَأْوَىٰ نُزُلًۢا بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ١٩ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فَسَقُوا۟
فَمَأْوَىٰهُمُ ٱلنَّارُ كُلَّمَآ أَرَادُوٓا۟ أَن يَخْرُجُوا۟ مِنْهَآ أُعِيدُوا۟ فِيهَا
وَقِيلَ لَهُمْ ذُوقُوا۟ عَذَابَ ٱلنَّارِ ٱلَّذِى كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ٢٠



**(12) Da sannu masu laifi zasu bayyana a gaban Allah ranar alqiyama, suna maqasqanta, suna sunkuyar da kawunansu, saboda kafircewar su da tashi bayan mutuwa, suna jin wulaqanta a tare da su, suna cewa: "Ya Ubangijin mu, haqiqa mun ga abin da muka kasance muna qaryatawa na tashi bayan mutuwa, kuma mun ji gaskiyar abin da Manzanni suka zo da shi daga gare ka, ka mayar da mu rayuwar duniya, zamu yi aiki nagari, wanda zai sa ka yarda da mu, yanzu mun tabbatar tashi bayan mutuwa, da gaskiya abin da Manzanni suka zo da shi. Da a ce zaka ga masu laifi, a wannan hali, da ka ga ka ga lamari mai girma.**

**(13) Da mun ga damar ba wa kowace rai shiriya, da datar da ita zuwa xaukan haka, da mun sa ta ta yi haka, sai dai zance ya tabbata daga gare ni a kan adalci da hikima cewa: "Tabbas za cika wutar Jahannama ranar alqiyama, da kafirai, daga cikin mutane da aljanu, domin sun zavar wa kansu hanyar kafirci da vata, sun bar hanyar imani, da daidaituwa".**

**(14) Za a ce musu ranar alqiyama, cikin wulaqantarwa: "Ku xanxani azaba, saboda rafkanarku a rayuwar duniya, game da haxuwarku da Allah, don yi muku hisabi. Mu ma mun barku a cikin azaba, ba tare da mun damu da wahalar da kuke sha, ku xanxani azabar wuta ta dindindin, wadda baya yankewa, saboda abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya na savon Allah.**

**Yayin da Allah ya gama bayanin halin masu laifi, sai kuma ya ambaci halin muminai, ya ce:**

**(15) Kaxai waxanda suke yin imani da ayoyinmu waxanda muka saukar ga Manzonmu, su ne waxanda idan an musu wa'azi sai su yi sujjada ga Allah, suna masu tsarkake shi da gode masa, ba sa yin girman kai da bauta masa, ko yi masa sujjada a kowane hali.**

**(16) Gefen jikinsu suna yin nisa daga shimfixunsu, waxanda suke barci a kansu, suna barinsu su fuskanci Allah, suna kiransa a cikin sallolinsu da sauran abubuwansu, suna masu tsoron azabarsa, suna kwaxayin rahamarsa, suna bada dukiyoyinsu waxanda muka ba su, saboda Allah.**

**(17) Babu wata rai da ta san haqiqanin abin da Allah ya tanadar musu, daga abin da idanuwansu za su sanyi da shi, sakamako ne daga wajen Allah zuwa gare su, saboda abin da suke aikatawa a duniya, na ayyuka nagartattu, wannan sakamako ne da ba wanda zai iya saninsa gaba xaya sai Allah, saboda girmansa.**

**(18) Duk wanda ya yi imani da Allah, yana mai aiki da umarnin sa, yana nisantar abubuwan da ya hana, ba daidai yake da wanda ya fita daga xa'ar Allah ba, ba za su yi daidai ba a wajen Allah da wajen sakamako.**

**(19) Amma waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki nagari, to, sakamakonsu, wanda aka tanadar musu shi ne, aljannatan da zasu tabbata a cikinsu, girmamawa ce daga Allah zuwa gare su, sakamako ne na abin da suka kasance suna aikatawa a duniya.**

**(20) Amma waxanda suka fita daga xa'ar Allah, ta hanyar kafirci da aikata savo, to matabbatarsu wadda aka tanadar musu ranar alqiyama, ita ce wuta, zasu zauna a cikinta har abada, duk lokacin da suka yi nufin fita daga cikinta, sai a dawo da su cikinta, a ce da su cikin wulaqantawa: "Ku xanxani azabar wutar da kuka kasance a duniya kuna qaryatawa da ita, yayin da Manzannin ku suke tsoratar da ku daga gare ta.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Imanin kafirai a ranar alqiyama, ba zai musu amfani ba, domin rana ce ta sakamako, ba ranar aiki ba.**

**2 - Haxarin rafkana daga haxuwa da Allah ranar alqiyama.**

**3 - Tsayuwar dare tana cikin tsarin Muminai.**

وَلَنُذِيقَنَّهُم مِّنَ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡأَدۡنَىٰ دُونَ ٱلۡعَذَابِ ٱلۡأَكۡبَرِ
لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ ٢١ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ ثُمَّ
أَعۡرَضَ عَنۡهَآۚ إِنَّا مِنَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ مُنتَقِمُونَ ٢٢ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا
مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ فَلَا تَكُن فِي مِرۡيَةٖ مِّن لِّقَآئِهِۦۖ وَجَعَلۡنَٰهُ
هُدٗى لِّبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٢٣ وَجَعَلۡنَا مِنۡهُمۡ أَئِمَّةٗ يَهۡدُونَ بِأَمۡرِنَا
لَمَّا صَبَرُواْۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يُوقِنُونَ ٢٤ إِنَّ رَبَّكَ هُوَ
يَفۡصِلُ بَيۡنَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ
٢٥ أَوَلَمۡ يَهۡدِ لَهُمۡ كَمۡ أَهۡلَكۡنَا مِن قَبۡلِهِم مِّنَ ٱلۡقُرُونِ
يَمۡشُونَ فِي مَسَٰكِنِهِمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٍۚ أَفَلَا يَسۡمَعُونَ
٢٦ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّا نَسُوقُ ٱلۡمَآءَ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ٱلۡجُرُزِ فَنُخۡرِجُ
بِهِۦ زَرۡعٗا تَأۡكُلُ مِنۡهُ أَنۡعَٰمُهُمۡ وَأَنفُسُهُمۡۚ أَفَلَا يُبۡصِرُونَ
٢٧ وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡفَتۡحُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٢٨
قُلۡ يَوۡمَ ٱلۡفَتۡحِ لَا يَنفَعُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِيمَٰنُهُمۡ وَلَا هُمۡ
يُنظَرُونَ ٢٩ فَأَعۡرِضۡ عَنۡهُمۡ وَٱنتَظِرۡ إِنَّهُم مُّنتَظِرُونَ ٣٠

آياتها ٧٣ — سُورَةُ الأَحۡزَابِ — ترتيبها ٣٣



**(21) Wallahi zamu xanxanawa waxannan masu qaryatawa, waxanda suka fita daga xa'ar Ubangijinsu, zamu xanxana musu jarraba da bala'o'i, a duniya, gabanin babbar azaba, wadda aka tanadar musu a lahira, in basu tuba ba, wataqila za su dawo zuwa ga xa'ar Ubangijinsu.**

**(22) Babu wanda ya kai zaluncin wanda aka tunatar da shi ayoyin Allah, amma bai wa'azantu ba, ya bijire mata, bai damu ba. Haqiqa mu, dangane da masu laifi, waxanda suke aikata kafirci da savo, da bijirewa ayoyin Allah, masu damqa ne, ba makawa.**

**(23) Haqiqa mun ba wa Annabi Musa Attaura. Ya kai wannan Manzo kada ka zama cikin shakku game da haxuwarka da Annabi Musa a daren Isra'i da Mi'iraji. Mun sanya littafin da muka saukarwa Annabi Musa ya zama shiriya ga Bani Isra'ila ne daga vata.**

**(24) Kuma mun sanya wasu jagorori a cikin Bani Isra'ila, waxanda ake koyi da su, suna shiryarwa zuwa ga gaskiya, bayan sun yi haqurin kamanta umarnin Allah, da nisantar abubuwan da ya hana, kuma suka yi haquri a kan cutar da su da aka yi a hanyar kira ga Allah, kuma sun kasance masu imani da ayoyin Allah da aka saukar musu ga Manzansu, gasgatawar da ba shakka.**

**(25) Haqiqa Ubangijinka - Ya kai wannan Annabi – shi ne zai hukunci tsakaninsu ranar alqiyama, cikin abin da suka kasance a duniya suna yin savani a kai, ya bayyana mai gaskiya, daga maras gaskiya, kuma ya sakawa kowa da abin da ya cancance shi.**

**(26) Shin waxannan sun makance ne, basu gane al'ummu nawa ne da suka gabace su waxanda muka halakar da su ba? Ga shi nan suna tafiya a cikin gidajensu, waxanda suke zaune a cikinsu kafin halakar da su, amma basu wa'azantu da halinsu ba. Lallai a cikin abin da ya faru ga waxancan al'ummu na halakarwa, saboda kafirci da savonsu, akwai izina da za a iya kafa hujja da su a kan gaskiyar Manzanninsu, waxanda suka zo musu daga wurin Allah. Yanzu waxannan masu qaryatawar basa sauraron ayoyin Allah, sauraro na karva da wa'azantuwa?.**

**(27) Shin waxannan masu qaryata tashi bayan mutuwa, basu ga yadda muke saukar da ruwan sama ga qasar da ta bushe, babu wani tsiro a kanta, sai mu fitar da shuka da wannan ruwa, raqumansu da shanunsu da tumakansu suna ci daga wannan shukar? Basa ganin haka ne? Basa fahimtar cewa: duk wanda zai iya fito da tsirrai a bayan qasar da ta bushe mai iko ne a kan raya matattu ba?.**

**(28) Masu qaryatawa da tashi bayan mutuwa, masu neman a gaggauta musu azaba suna cewa: "Yaushe ne wannan hukuncin da kuke riya cewa zai raba gardama a tsakaninmu da ku a ranar alqiyama?. makomar mu ta kasance wuta, ku kuma makomarku ta kasance Aljannah?!.**

**(29) Ya kai wannan Manzo, ka ce musu: "Wannan alqawari shi ne ranar alqiyama, ita ce ranar rarrabewa a tsakanin bayi, ranar da waxanda suka kafirta a duniya gasgatawarsu bayan ganin ranar alqiyama ba zata yi musu amfani ba, kuma ba za a jirkinta musu ba, don su tuba zuwa ga Ubangijinsu, su koma zuwa gare shi.**

**(30) Ya kai wannan Manzo ka kawar da kanka ga barin waxannan, bayan sun ci gaba da vatansu, ka saurari abin da zai same su, su ma suna jiran abin da ka yi musu alqawari na azaba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Azabtar da kafiri a duniya wata hanya ce ta tubansa.**

**2 - Tabbatar da gamuwa tsakanin Annabi Musa da Annabinmu Muhammad (S.A.W) a daren isra'i da mi'iraji. Haquri da yaqini, siffofi ne guda biyu na jagorori a cikin addini.**

# Suratul Ahzab

An Saukar Da Ita A Madinah



بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ ٱتَّقِ ٱللَّهَ وَلَا تُطِعِ ٱلۡكَٰفِرِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقِينَۚ إِنَّ
ٱللَّهَ كَانَ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١ وَٱتَّبِعۡ مَا يُوحَىٰٓ إِلَيۡكَ
مِن رَّبِّكَۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ٢ وَتَوَكَّلۡ
عَلَى ٱللَّهِۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ وَكِيلٗا ٣ مَّا جَعَلَ ٱللَّهُ لِرَجُلٖ مِّن
قَلۡبَيۡنِ فِي جَوۡفِهِۦۚ وَمَا جَعَلَ أَزۡوَٰجَكُمُ ٱلَّٰٓـِٔي تُظَٰهِرُونَ
مِنۡهُنَّ أُمَّهَٰتِكُمۡۚ وَمَا جَعَلَ أَدۡعِيَآءَكُمۡ أَبۡنَآءَكُمۡۚ ذَٰلِكُمۡ قَوۡلُكُم
بِأَفۡوَٰهِكُمۡۖ وَٱللَّهُ يَقُولُ ٱلۡحَقَّ وَهُوَ يَهۡدِي ٱلسَّبِيلَ ٤
ٱدۡعُوهُمۡ لِأٓبَآئِهِمۡ هُوَ أَقۡسَطُ عِندَ ٱللَّهِۚ فَإِن لَّمۡ تَعۡلَمُوٓاْ ءَابَآءَهُمۡ
فَإِخۡوَٰنُكُمۡ فِي ٱلدِّينِ وَمَوَٰلِيكُمۡۚ وَلَيۡسَ عَلَيۡكُمۡ جُنَاحٞ فِيمَآ
أَخۡطَأۡتُم بِهِۦ وَلَٰكِن مَّا تَعَمَّدَتۡ قُلُوبُكُمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ
غَفُورٗا رَّحِيمًا ٥ ٱلنَّبِيُّ أَوۡلَىٰ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ مِنۡ أَنفُسِهِمۡۖ
وَأَزۡوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمۡۗ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ
فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ إِلَّآ أَن تَفۡعَلُوٓاْ إِلَىٰٓ
أَوۡلِيَآئِكُم مَّعۡرُوفٗاۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَسۡطُورٗا ٦



## Daga Manufofin Surar:

**Surar ta mayar da hankali wajen bayanin irin kulawar da Allah yake ba Annabinsa (S.A.W) da kariya gare shi da iyalan gidansa.**

## Tafsir:

**(1) Ya kai wannan Annabi, ka tabbata kai, da waxanda suke tare da kai a kan tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, ka ji tsoronsa shi kaxai, kada ka bi kafirai da munafikai cikin son zuciyarsu. Haqiqa Allah Masani ne ga abin da kafirai da munafikai suke shiryawa na makirci, mai hikima ne a cikin halittarsa, da tsarinsa.**

**(2) Ka bi abin da Ubangijinka yake saukar maka na wahayi. Haqiqa Allah masani ne mai bada labari ga abin da kuke aikatawa, babu wani abu da yake kuvuce masa, kuma zai yi muku sakayya a kan ayyukanku.**

**(3) Kuma ka dogara ga Allah shi kaxai, a cikin duk lamuran ka, Allah ya isa ya zama mai bada cikakkiyar kulawa ga duk wanda ya dogara gare shi, cikin bayinsa.**

**(4) Kamar yadda Allah bai halicci zuciya biyu ba a qirjin mutum guda, haka ma bai sanya matan aure su zama a matsayin iyaye mata ba, wajen haramcin a aure su, kuma bai sanya 'ya'yan riqo su zama tamkar 'ya'ya na tsatso ba, haqiqa Zihari – shi ne mutum ya haramtawa kansa matarsa ta aure – haka nan jivintar wani xa (da mayar da shi kamar xan da mutum ya haifa) duka waxannan abubuwa guda biyu (Zihari da Jivintar xa) suna cikin al'adun jahiliyya, waxanda musulunci ya hana yin su. Zihari da da jivintar xa maganganu ne kawai da kuke maimaitawa da harshen ku, amma ba gaskiya ba ne, matar aure ba uwa ba ce, haka na xan riqo ba xa ne na haqiqa ba, Allah yana faxin gaskiya don bayinsa su yi aiki da ita, kuma yana shiryarwa zuwa ga tafarkin gaskiya.**

**(5) Waxanda ku ke riya cewa: 'ya'yan ku ne, ku danganta su zuwa ga iyayensu na asali, yin hakan shi ne adalci har a wurin Allah, idan kuma baku san iyayensu na asali ba, waxanda zaku danganta su zuwa gare su, to su 'yan uwanku ne a addini, kuma waxanda kuka 'yanta su daga bauta, kuna iya kiransu, ku ce: ya kai xan uwana, ko ya kai xan baffa na. Babu laifi a kanku idan xayanku ya yi kuskure,ya danganta xan riqo zuwa ga wanda yake riqonsa, zan yi laifi ne idan da gangan ya aikata. Allah ya tabbata mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai jin qansu, ta inda baya kama su idan sun yi kuskure.**

**(6) Annabi Muhammad (S.A.W) ya fi Muminai cancanta da kansu, cikin duk abin da ya kira su zuwa gare shi, koda kuwa zukatansu suna karkata ga waninsa, kuma matansa (S.A.W) a matsayin iyaye suke ga dukkan Muminai, don haka ya haramta a kan duk wani Mumini ya auri wata daga cikin su bayan mutuwar Annabi (S.A.W). 'Yan uwan juna sashensu ya fi cancanta da sashe a wurin gado, a cikin hukuncin Allah, fiye da ma'abota imani da waxanda suka yi hijira saboda Allah, waxanda suka kasance suna gadon juna a tsakaninsu a farkon musulunci, sai aka shafe yin gadonsu daga baya, sai dai idan ku Muminai kun yi wa masoyanku, waxanda ba su da gado alheri, na yi musu wasiyya da kyautata musu, to hakan ya halatta. Wannan hukunci yana nan a rubuce a cikin Lauhul Mahfuz, don haka aiki da shi ya wajaba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Babu wanda ya girmi a yi masa umarni da kyakkyawan aiki, ko a hana shi aikata mummuna.**
**2 - Wannan al'umma ba a kama ta da kuskure. 3 - Wajabcin gabatar da muradin Annabi (S.A.W) a kan muradin zuciya. 4 - Bayanin matsayin matan Annabi (S.A.W), da haramcin aurar su bayan Annabi (S.A.W), don su iyayen Muminai ne.**

وَإِذْ أَخَذْنَا مِنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مِيثَٰقَهُمْ وَمِنكَ وَمِن نُّوحٍ وَإِبْرَٰهِيمَ
وَمُوسَىٰ وَعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ ۖ وَأَخَذْنَا مِنْهُم مِّيثَٰقًا غَلِيظًا ٧
لِّيَسْـَٔلَ ٱلصَّٰدِقِينَ عَن صِدْقِهِمْ ۚ وَأَعَدَّ لِلْكَٰفِرِينَ عَذَابًا أَلِيمًا
٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَةَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ جَآءَتْكُمْ
جُنُودٌ فَأَرْسَلْنَا عَلَيْهِمْ رِيحًا وَجُنُودًا لَّمْ تَرَوْهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ
بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرًا ٩ إِذْ جَآءُوكُم مِّن فَوْقِكُمْ وَمِنْ أَسْفَلَ
مِنكُمْ وَإِذْ زَاغَتِ ٱلْأَبْصَٰرُ وَبَلَغَتِ ٱلْقُلُوبُ ٱلْحَنَاجِرَ
وَتَظُنُّونَ بِٱللَّهِ ٱلظُّنُونَا۠ ١٠ هُنَالِكَ ٱبْتُلِىَ ٱلْمُؤْمِنُونَ وَزُلْزِلُوا۟
زِلْزَالًا شَدِيدًا ١١ وَإِذْ يَقُولُ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم
مَّرَضٌ مَّا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ إِلَّا غُرُورًا ١٢ وَإِذْ قَالَت طَّآئِفَةٌ
مِّنْهُمْ يَٰٓأَهْلَ يَثْرِبَ لَا مُقَامَ لَكُمْ فَٱرْجِعُوا۟ ۚ وَيَسْتَـْٔذِنُ فَرِيقٌ
مِّنْهُمُ ٱلنَّبِىَّ يَقُولُونَ إِنَّ بُيُوتَنَا عَوْرَةٌ وَمَا هِىَ بِعَوْرَةٍ ۖ إِن يُرِيدُونَ
إِلَّا فِرَارًا ١٣ وَلَوْ دُخِلَتْ عَلَيْهِم مِّنْ أَقْطَارِهَا ثُمَّ سُئِلُوا۟ ٱلْفِتْنَةَ
لَءَاتَوْهَا وَمَا تَلَبَّثُوا۟ بِهَآ إِلَّا يَسِيرًا ١٤ وَلَقَدْ كَانُوا۟ عَٰهَدُوا۟
ٱللَّهَ مِن قَبْلُ لَا يُوَلُّونَ ٱلْأَدْبَٰرَ ۚ وَكَانَ عَهْدُ ٱللَّهِ مَسْـُٔولًا ١٥



**(7) Ka ambata - Ya kai wannan Annabi -lokacin da muka riki alqawari mai qarfi daga Annabawa, a kan su bautata Allah shi kaxai, kada su yi shirka da shi, kuma su isar da abin da aka saukar musu na wahayi, mun riqi wannan alqawari daga gare ka a keve, haka ma daga Annabi Nuhu, da Ibrahim, da Isa xan Maryam, duk mu riqi alqawari mai qarfi a kan su cika amanar da aka xora musu, ta isar da saqonnin Allah.**

**(8) Allah ya riki wannan alqawari mai qarfi daga Annabawa, don ya tambayi masu gaskiya daga Manzanni game da gaskiyar su, kuma ya zama tsoratarwa ga kafirai. Allah ya tanadarwa waxanda suka kafircewa masa da Manzanninsa, azaba mai raxaxi ranar alqiyama, ita ce wutar Jahannama**

**(9) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta, ku tuna ni'imar Allah da ya yi muku, yayin da rundononin kafirai waxanda suka haxu don yaqarku suka zo Madina, kuma Munafikai da yahudawa suna taimaka musu, sai muka aiko musu da wata iska – mai suna Sabaa – wanda aka taimaki Annabi (S.A.W) da ita, kuma muka aiko da rundunar Mala'iku, waxanda baku gansu ba, sai kafirai suka bada baya suna da gudu, suka kasa yin komai. Haqiqa dangane da abubuwan da kuke aikatawa mai gani ne, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai saka muku a kan ayyukanku.**

**(10) Wannan ya faru a lokacin da Kafirai suka zo muku ta saman kwarin (rami), da qasan sa, da vangaren gabas da yamma, a lokacin ne idanuwa suka daina ganin komai sai abokan gabarsu, zukata suka kawo maqoshi, saboda tsabar tsora, kuka yi ta zace zace iri-iri ga Allah, wani lokacin ku yi zaton samun nasara, wani lokacin ku yi zaton rashinta.**

**(11) A wannan yanayi na yaqin khandaq (Yaqin Gwalalo), an jarrabi muminai da abin da suka gamu da shi na taron abokan gaba a kansu, suka rikice, rikicewa mai tsanani, saboda da tsananin tsoro, muminai na gaskiya suka bayyana daga munafukai, aka gane kowa da kowa.**

**(12) A wannan rana sai munafikai da masu raunin imani, waxanda akwai shakka a zukatansu suka ce: "Alqawarin da Allah da Manzo suka yi mana na samun nasara a kan abokan gabanmu, da tabbata a bayan qasa, ba komai ba ne face qarya, wadda bata da tushe.**

**(13) Ya kai wannan Manzo ka ambaci yayin da wasu daga cikin munafikan Madinah suka ce: "Ya ku mutanen Yasriba(Sunan Madinah ne kafin zuwan musulunci) ba ku da wurin sauka a gindin dutsen Sal'i, kusa ramin gwalalo, don haka ku koma gidajenku". Wasu daga cikinsu suna neman izini daga Annabi (S.A.W) ya basu dama su koma gidajensu, suna da'awar gidajensu a buxe suke ga abokan gaba, alhali ba a buxe suke ba, kawai suna son guduwa ne daga abokan gaba da wannan uzurin na qarya**

**(14) Da a ce abokan gabar za su shigo musu Madinah ta kowane saqo, kuma su nemi su dawo zuwa ga kafirci da shirka da Allah, da sun yi aikata haka, ba za su qi yin ridda da komawa kafirci ba sai yan kaxan daga cikinsu.**

**(15) Haqiqa waxannan Munafikai sun yi wa Allah alqawari, bayan sun gudu daga yaqi ranar Uhud, suka ce: "Idan ya nuna musu wani yaqin, lallai za su yaqi abokan gabarsu, kuma ba zasu gudu ba don tsoron abokan gaba, sai dai sun warware wannan alqawarin na su. Tabbas bawa abin tambaya ne game da alqawarin da ya xauka tsakaninsa da Allah, kuma da sannu za a tambaye shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Matsayin Ulul azmi cikin Annabawa.**
**2 - Qarfafar da Allah yake yi wa Muminai, yayin saukar tsanani.**
**3 - Yadda Munafikai suke tavar da Muminai yayin da wata jarrabawa ta taso.**

قُل لَّن يَنفَعَكُمُ ٱلۡفِرَارُ إِن فَرَرۡتُم مِّنَ ٱلۡمَوۡتِ أَوِ ٱلۡقَتۡلِ وَإِذٗا
لَّا تُمَتَّعُونَ إِلَّا قَلِيلٗا ١٦ قُلۡ مَن ذَا ٱلَّذِي يَعۡصِمُكُم مِّنَ ٱللَّهِ
إِنۡ أَرَادَ بِكُمۡ سُوٓءًا أَوۡ أَرَادَ بِكُمۡ رَحۡمَةٗۚ وَلَا يَجِدُونَ لَهُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ١٧ ۞ قَدۡ يَعۡلَمُ ٱللَّهُ ٱلۡمُعَوِّقِينَ مِنكُمۡ وَٱلۡقَآئِلِينَ
لِإِخۡوَٰنِهِمۡ هَلُمَّ إِلَيۡنَاۖ وَلَا يَأۡتُونَ ٱلۡبَأۡسَ إِلَّا قَلِيلًا ١٨ أَشِحَّةً
عَلَيۡكُمۡۖ فَإِذَا جَآءَ ٱلۡخَوۡفُ رَأَيۡتَهُمۡ يَنظُرُونَ إِلَيۡكَ تَدُورُ أَعۡيُنُهُمۡ
كَٱلَّذِي يُغۡشَىٰ عَلَيۡهِ مِنَ ٱلۡمَوۡتِۖ فَإِذَا ذَهَبَ ٱلۡخَوۡفُ سَلَقُوكُم
بِأَلۡسِنَةٍ حِدَادٍ أَشِحَّةً عَلَى ٱلۡخَيۡرِۚ أُوْلَٰٓئِكَ لَمۡ يُؤۡمِنُواْ فَأَحۡبَطَ
ٱللَّهُ أَعۡمَٰلَهُمۡۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٗا ١٩ يَحۡسَبُونَ
ٱلۡأَحۡزَابَ لَمۡ يَذۡهَبُواْۖ وَإِن يَأۡتِ ٱلۡأَحۡزَابُ يَوَدُّواْ لَوۡ أَنَّهُم
بَادُونَ فِي ٱلۡأَعۡرَابِ يَسۡـَٔلُونَ عَنۡ أَنۢبَآئِكُمۡۖ وَلَوۡ كَانُواْ فِيكُم
مَّا قَٰتَلُوٓاْ إِلَّا قَلِيلٗا ٢٠ لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ
لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا ٢١
وَلَمَّا رَءَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلۡأَحۡزَابَ قَالُواْ هَٰذَا مَا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
وَصَدَقَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥۚ وَمَا زَادَهُمۡ إِلَّآ إِيمَٰنٗا وَتَسۡلِيمٗا ٢٢



**(16) Ka cewa waxannan - Ya kai wannan Manzo -: “Guduwa daga yaqi ba zai amfana muku komai ba, in kun gudu daga yaqin ne don tsoron mutuwa, ko kisa, don ajali a qaddare yake, kuma idan kuka gudu, amma lokacin mutuwarku bai yi ba, to, ba wani daxi da zaku ji face xan lokaci kaxan.**

**(17) Ka gaya musu - Ya kai wannan Manzo -: “Waye zai kare ku daga Allah idan ya nufe ku da abin da kuke qi na mutuwa ko kisa, ko ya yi nufe ku da abin da zai amfane ku na alheri da kuvuta?. Ba wanda zai kare ku daga haka, sannan waxannan Munafikai ba zasu samu wani koma bayan Allah wanda zai jivinci lamarinsu ba, ko wani mataimaki da zai kare su daga uqubar Allah.**

**(18) Allah ya san masu kashewa wasu gwiwa daga cikinku wajen fita yaqi, tare da Manzon Allah (S.A.W), da waxanda suke cewa ‘yan uwansu: “Ku zo wurin mu, kada ku yi yaqi tare da shi, don kada a kashe ku, haqiqa muna ji muku tsoron kisa”. Waxannan masu kashewa mutane gwiwar, su ma basa zuwa yaqi sai xan kaxan, don su kare kansu daga abin kunya, ba don su taimaki Allah da Manzonsa ba.**

**(19) Masu yi muku rowa ne - Ya ku Muminai – da dukiyoyinsu, ba za su taimaka muku bayar da ita ba, kuma rowar rayukansu ne, baza su yi yaqi tare da ku ba, kuma marowata ne ga nuna muku qauna, ba za su qauna ce ku ba, idan abin tsoro ya zo, yayin gamuwa da abokan gaba, sai ka ga suna kallonka – Ya kai wannan Manzo – idanuwansu suna juyawa, saboda tsoro, kamar yadda idanun wanda yake cikin mayen mutuwa suke juyawa, idan tsoron ya tafi daga gare su, suka samu nutsuwa, sai su cutar da ku da maganganu marasa kyau da bakunansu, suna masu yi muku rowar ganima, suna neman inda take. Masu waxannan siffofi ba su yi imani na haqiqa ba, don haka sai Allah ya vata ladan ayyukansu. Wannan vatawar abu ne mai sauqi a wurin Allah.**

**(20) Waxannan matsoratan suna zaton waxannan qungiyoyin da suka taru don yaqar Manzon Allah (S.A.W) da yaqar Muminai, ba za su tafi ba, har sai sun gama da Muminai. Kuma da za a qaddara waxannan rundononi su zo karo na biyu, da waxannan munafikai sun yi burin ina ma suna wajen Madinah tare da larabawan qauye, suna tambayar labarukanku, me ya faru da ku bayan abokan gabarku sun yaqe ku?. Da suna tare da ku – Ya ku Muminai – da baza su yi yaqi tare da ku ba, sai xan kaxan, don haka kada ku damu da su, kada ku yi baqin ciki a kansu.**

**(21) Kuna da abin koyi cikin abin da Manzon Allah (S.A.W) ya faxa, da abin da ya aikata, kyakkyawan abin koyi, saboda ya zo yaqi da kansa mai daraja, ya yi yaqi, to ta yaya ku zaku rowar rayukanku bayan haka?. Ba wanda yake koyi da Manzon Allah (S.A.W) sai wanda yake kwaxayin gidan lahira, kuma ya yi aiki don haka, ya ambaci Allah da yawa. Amma wanda baya kwaxayin gidan lahira, baya ambaton Allah da yawa, to wannan baya koyi da Manzon Allah (S.A.W)**

**(22) Yayin da Muminai suka ga waxannan rundunoni, waxanda suka haxu don yaqar su, sai suka ce: “Wannan shi ne abin da Allah da Manzonsa suka yi mana alqawarin zai faru na jarrabawa da samun nasara, kuma Allah da Manzo sun yi gaskiya a kan haka, ga shi ya faru, don haka wannan rundononi da suka gani, babu abin da hakan ya qara musu sai imani da Allah da jayuwa zuwa gare shi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Ajali a qayyade yake, yaqi ba ya kusanto da shi, haka kuma gudu baya jinkirtar da shi. 2 - Kashe gwiwar mutane wurin yin jihadi, halin Munafukai ne a koda yaushe. 3 - Annabi (S.A.W) shi ne abin koyin Muminai, cikin maganganunsa, da ayyukansa.**
**4 - Sakankancewa da Allah, da kuma jayuwa gare shi, siffa ce daga cikin siffofin Muminai.**

مِّنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ رِجَالٌ صَدَقُوا۟ مَا عَٰهَدُوا۟ ٱللَّهَ عَلَيْهِ ۖ فَمِنْهُم مَّن
قَضَىٰ نَحْبَهُۥ وَمِنْهُم مَّن يَنتَظِرُ ۖ وَمَا بَدَّلُوا۟ تَبْدِيلًا ﴿٢٣﴾ لِّيَجْزِىَ
ٱللَّهُ ٱلصَّٰدِقِينَ بِصِدْقِهِمْ وَيُعَذِّبَ ٱلْمُنَٰفِقِينَ إِن شَآءَ أَوْ
يَتُوبَ عَلَيْهِمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورًا رَّحِيمًا ﴿٢٤﴾ وَرَدَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُوا۟ بِغَيْظِهِمْ لَمْ يَنَالُوا۟ خَيْرًا ۚ وَكَفَى ٱللَّهُ ٱلْمُؤْمِنِينَ
ٱلْقِتَالَ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ قَوِيًّا عَزِيزًا ﴿٢٥﴾ وَأَنزَلَ ٱلَّذِينَ ظَٰهَرُوهُم مِّنْ
أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ مِن صَيَاصِيهِمْ وَقَذَفَ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلرُّعْبَ
فَرِيقًا تَقْتُلُونَ وَتَأْسِرُونَ فَرِيقًا ﴿٢٦﴾ وَأَوْرَثَكُمْ أَرْضَهُمْ
وَدِيَٰرَهُمْ وَأَمْوَٰلَهُمْ وَأَرْضًا لَّمْ تَطَـُٔوهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَىْءٍ قَدِيرًا ﴿٢٧﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ إِن كُنتُنَّ تُرِدْنَ
ٱلْحَيَوٰةَ ٱلدُّنْيَا وَزِينَتَهَا فَتَعَالَيْنَ أُمَتِّعْكُنَّ وَأُسَرِّحْكُنَّ
سَرَاحًا جَمِيلًا ﴿٢٨﴾ وَإِن كُنتُنَّ تُرِدْنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلدَّارَ
ٱلْءَاخِرَةَ فَإِنَّ ٱللَّهَ أَعَدَّ لِلْمُحْسِنَٰتِ مِنكُنَّ أَجْرًا عَظِيمًا ﴿٢٩﴾
يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِىِّ مَن يَأْتِ مِنكُنَّ بِفَٰحِشَةٍ مُّبَيِّنَةٍ يُضَٰعَفْ
لَهَا ٱلْعَذَابُ ضِعْفَيْنِ ۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرًا ﴿٣٠﴾



**(23) Daga cikin Muminai akwai wasu mazaje da suka yi wa Allah gaskiya, suka cika Alqawarin da su ka yi masa, na tabbata da haquri a kan jihadi a tafarkin Allah. Daga cikinsu akwai waxanda suka mutu, ko aka kashe su akan tafarkin Allah, kuma akwai waxanda suke jiran shahada a tafarkin Allah, waxannan muminai ba su canza abin da suka yi Allah alqawari ba, kamar yadda munafikai suka yi da alqawuransu.**

**(24) Domin Allah ya sakawa masu gaskiya, waxanda suka cika alqawarin da suka xaukar wa Allah, da gaskiyar su da cika alqawarinsu, kuma ya azabtar da Munafikai, masu warware alqawuransu, idan ya ga dama, ta hanyar ya kashe su gabanin su tuba daga kafircin su, ko kuma ya datar da su, su tuba. haqiqa Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga zunubansa, kuma mai yawan jinqai ne a gare shi.**

**(25) Allah ya mayar da qabilar Quraishawa da Gaxfan, da waxanda suke tare da su, da baqin cikinsu da damuwarsu, da baqin, saboda rashin samun abin da suka yi buri, ba su ci nasarar abin da suka yi nufi ba, na gamawa da Muminai ba, Allah ya isar wa Muminai yin yaqi da su, da abin da ya turo na iska, da abin da ya saukar na Mala'iku. Haqiqa Allah mai qarfi ne, kuma Mabuwayi ne, babu wanda ya isa ya yi galaba a kansa face sai ya rinjaye shi, kuma ya qasqanta shi.**

**(26) Kuma Allah ya saukar da waxanda suka taimake su, cikin Yahudawa daga ganuwar su da suke vuya a cikinta daga abokan gabarsu, ya jefa musu tsoro a zukatan su, har ya zamanto ku Muminai kuna kashe wasu daga cikinsu, kuna kama wasu ribatattun yaqi.**

**(27) Allah ya mallaka muku gonakinsu bayan halakar su da abin da yake cikinsu na shuke-shuke da dabino, kuma ya mallaka muku gidajen su, da wasu dukiyoyin su, ya mallaka muku qasar khaibar, wadda har yanzu baku taka ta ba, amma nan gaba zaku taka ta, wannan alqawari ne da bushara ga Muminai. Haqiqa Allah mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gajiyar da shi.**

**(28) Ya kai wannan Annabi, ka faxa wa matanka, yayin da suka nemi ka yalwata musu a wajen ciyarwa, kuma alhali ba kada abin da zaka yalwata musu da shi, to ka ce da su: "Idan rayuwar duniya da adon ta kuke so, to, ku zo in jiyar da ku daxin da ake jiyar da waxanda aka saki, sannan sai na sake ku, saki wanda babu cutarwa a cikinsa.**

**(29) Idan kuwa kun kasance kuna son yardar Allah da Manzonsa ne, kuma kuna son Aljannah a gidan lahira, to ku yi haquri da yanayin da kuka samu kanku a ciki. haqiqa Allah ya tanadar wa wadda ta kyautata a cikinku, ta hanyar haquri da kyakkyawan zama lada mai girma.**

**(30) Ya ku matan Annabi, duk wadda a cikinku ta zo da alfasha bayyananniya, to za a ninka mata azaba ranar alqiyama ninki biyu, saboda matsayinta, da darajarta, da kuma kare vangaren Annabi (S.A.W).Wannan ninkawar abu ne mai sauqi a wurin Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsarkakewar Allah ga sahabban Manzon Allah (S.A.W), wanda wannan matsayi ne mai girma gare su.**
**2 - Taimakon Allah ga bayinsa, ta inda ba sa zato, matuqar sun ji tsoron Allah.**
**3 - Mummunan qarshen yaudarar Yahudawan waxanda suka taimaki rundunonin da suka zo yaqi.**
**4 - Zavar yardar Allah da Manzonsa da matan Annabi (S.A.W) suka yi, dalili ne da yake nuna qarfin imaninsu.**